🌕⚜️DA'IMAN⚜🌕
Na
MAMUH GEEE
☆dedicated to☆
Husnah bbchoudiallo
BISMILLAHIR-RAHMANR-RAHEEM.
Ina mika dukkanin godiata ga masoyana masu son novels dina,
Kuma akoyaushe ina samun sakon fatar alkhairanku...ngd allah yabar kauna.
1→5
Sallama take kwadowa tun akofar gidan harta shigo dan karamin tsakar gidan.
Sanye takeda atampha `yar leda kalar kore shar wato kalar asalin `dan `kauye..sai wani gyale fari data yafo mai bakin lesi da `yar jakar hannunta `baka data farfashe alamar tsufa duk da itace tafi kowa wayewa akauyen tunda itake zuwa birni.
Shekarunta xasu kai talatin da takwas zuwa da arba'in zuwa da sama.
Wata sallamar takuma kwadawa tana fadin,
Wai duka gidan bakowane nake sallama ba'a amsawa?
Daga bayanta taji an amsa mata cikin wata yar siririyar murya.
Juyowa tayi adan tsorace tana ganinta ta hade fuska tareda watsa mata harara tace,
Lallai na yarda da kinsamu sake a wurin ladingo.
Munafuka mai kamada mayyar uwarta ace kina cikin gidan nan naketa rangada sallama amma kikayi lukus a daki.
Toma wai uwar me kike adakin ne.
Sunkuyar da kanta tayi muryarta na `dan rawa tace,
Kiyi hkr iya jummai wlh kainane yake ciwo banjiba.
To dama ina zakiji ladingo ta daure miki gindin iya shege.
Ladingon ce tafito daki cikin sauri tana daurawa guiguyayen kanta dankwali murya cikeda masifa tace,

Wai hayaniyar me nakejine a gidan?
Washe jajayen hakoranta tayi dasuka dafe tana fadin,
Aa jummai Ify daga zuwanki kike fada,badai wannan mai kamada muciyarce ta tabakiba yanxu nasa buba ya yayi mata dukan shanu ba. Aa kyaleta ai dagayau kuma andaina dukanta dan nazo mana da mafita akanta kuma wllh ba karamin samu zamuyiba ke wlh har makka sai munje.
Washe baki ladingo tayi cikeda farin ciki tace,
Haba jummai yanxu naji zanje,
Nidai idan xamu samu kudin aiko gidan cire kaine xan bada ita na huta da ganin wannan shegiyar fuskar tata mai kama da jariran aljanu.
`Dakin ladingo suka shige.
Tadan leko tace,
Kuma wlh kafin nafito ki tabbatarda kinyi wanke wanke kin dora mun abincin saidawata na rana.munafuka dangin ifiritu.
Sum sum tawuce tafara hada kayan wanke wanke dan ita tarigada tasaba da xagi,cin zarafi,duka da wahalar babah ladingo da `yayanta buba da idi dakuma babbar aminiyarta wato iya jummai.
○○○○○○○○
Gyara zama tayi takalli aminiyar tata tace,
Ladingo wani alherine nagani nace to lallai kece kika cancanta dashi.
Wato can gidan hajiyar danake zuwa birni kai mata yan aiki.
Da sauri ladingo ta kada kai tace inajinki jummai.
Wato wani alhajine mai shegen kudi a acan habuja, `dansa dayafiso fiyeda komai aduniyarnan yasamu matsala ta tabin kwakwalwa ta sanadin shan ko menene ma sunan?ni namanta sunan abun.
Mahaifiyar yaron ta rasu tun yana yaro ta a kasar turawa yatashi acan yakoyi shan abun har yasamu matsala.
Matar alhajin ita tace bazata iyaba shinefa akayi takai masu aiki duk wadda aka kai giduwa

suke basu iyawa sbd.
Mahaifin yaron kuma bai cika zamaba.
Anyi na asibin tarsun gaji shine aka kira malami yace sammu ne akayiwa yaron.
Atakaice dai baasamu me iya zama dashiba shine malamin yace ayi masa aure sbd matarsa bazata gujesaba.
Anyi neman matar dazaa aura masa babu sbd kowa tsoro yake.
To matar alhajin saita bugowa hajiyar danake zuwa gurinta tace asamo masa koda yar kauyece idan yaso inya warke sai ya saketa.kuma ta bada kyautar miliyan daya ga duk wanda yabada 'yarsa aka daurawa yaron.
Shine naga wannan mai kamada masillar kitson batada wani amfani agareki ba gwara ki badata ki hutada dangin mayuba.
Wani irin fitsarine yakusa kufcewa ladingo ta waro ido jikinta na rawa tace,
Jummai miliyan daya?
Yazamuyi dasu?
Kwantar da hankalinki
Miliyan daya dinnan rabawa zamuyi muda 'yayanmu tunda duk babu mai abinyi acikinsu sai sace sace kinga kuwa mun huta.
Wata irin guda ladingo tasaki tana shewa tace,
Wllh jummai idan kinje yau kice nabasu ita ko gobe sukeso suxo adaura nabasu........
🌕⚜️DA'IMAN⚜🌕

Na

MAMUH GEEE

☆dedicated to☆
Husna bbchoudiallo

6→10
Cikeda farin ciki tareda kwarin gwiwa ta isa kano gidan haj salamatu ta zayyane mata ansamu yarinyar daza'a daura auren da ita.
Cikin farin ciki itama haj salamatu takira matar alhajin haj zeenat tafada mata ansamu.
Murna tayi sosai tareda cewa,
To shikenan yanxu zan aiko da kudi dubu dari biyar asiyawa yarinyar kaya,

Kuma akoya mata abubuwan daya kamata dan nan dataxo babu me lokacin koya mata yanda zatayi aiki da abu kuma inson tadanyi clean kafin nanda sati sbd daddynsa dayazo za'azo adaura auren aranar juma'a.
So banason yazo yaganta kaca kaca yace anfasa dan gskia baxan iya cigaba da wahalar nema masa masu kula dashi.
Kuma inason tazo nan kano gidanki ace kece uwarta dan banasan yasan 'yar kauyece.
Kin gane zance kuwa.

Cikin rawar jiki tace,
Ai duk abunda kika fada kamar angamane haj.
Yauwa to sai anjimanku.

Tana datse kiran haj salamatu takalli jummai tace,
To jummai kindai ji abunda tace dan haka ya kike ganin xaayi da iyayen yarinyar?

Cikin washe baki jummai tace,
Ai haj ita yarinyar batada kowa sai matar mahaifinta data bada ita wato aminiyata sbd uwar yarinyar tarasu kuma batada dangi sbd buxuwace daga nijar ta tsallako wai iyayenta gobara ta cinyesu shinefa mijin aminiya ta ladingo ya aureta suka haifi yarinyar.
Bayan haihuwar yarinyar awuein haihuwa ta biyu ta rasu batareda ta haihun ba.
Bayan rasuwarta da shekara bakwai shima malam din yarasu sai yarinyar ta taso hannun aminiyata ladingo.
Kuma haj yarinyar shegen kyau ne da ita kamar jikar aljanu ga gashi kamar ka ara kayi kitso dashi,sannan duk kauyen nan ita kadai tayi karatu dan malam kafin yarasu dakansa yake kaita yadaukota.

Wata irin dariyar farin ciki haj salamt tayi tace,
Gaskia shiyasa nake yaba miki jummai dan kin iya xaben kwarai
Ta shekarar yarinyar nawa?kuma yaya sunanta?

Shekararta goma sha shida kuma sunanta NAZLI.

********
Karfe uku a kauyen takai tayi musu cikin gidan babah ladingo.
Kudi masu yawa kimanin dubu hamsin haj salamatu ta zubewa ladingo agabanta tace,
Wannan somin tabine na abani yarinyar naje da ita nafara shiryata kafin sati saiku samemu acan kano sai a daura auren acan suwuce da ita.

Idi ne yayi saurin waftar kudin yace,
Ai dama ko bakizo yau daukartaba mun shirya kaita gobe dan kawai ayi auren mu musamu kudin shanawa.
Buba yace,
Nidai kubani kasona na wannan daaka kawo natafi dan inada gurin xuwa kafin akawo masu

yawar.
Ladingo kuwa kwalawa nazli dake tsakar gidan tana jibgar wankin ladingo hardana buba da idi kira tayi tana xuwa ta durkusa kofar dakin cikin nutsuwa da sanyin murya tace,
Gani.
Maza je kihada tsummanki birni xamu yanxu.
Rass gabanta ya buga dan tasan abunda suke niyar yi mata na aura mata mai tabin hankali dantayi jinyarsa akan kudi sbd taji firarsu lkcin datake fadawa su buba jia.
Kwana tayi tana kuka dan ta kara tabbatarda rashin gatanta amma bazata bijire mataba dan kota bijire din to ta tabbatarda korarta zasuyi a gidan data rasa gurin zuwa gwara tabi umarninsu ko kashe tane marar Ifyar yayi ta huta da bakin ciki da azabar datake ciki.

Amotar haj salamatu sukazo har ladingo din dan tace itace uwar amarya sai andaura aure zata koma.

⚜⚜⚜⚜⚜⚜

Satinsu daya a kano kuma ayaune ake daura auren bayan anyi komai na neman aure a gun mijin haj salamatu dan shima lashe money ne bare dayaji 'dan hamshakin mai kudin nanne ALH ZAID OMAR.

Duk wani abunda akeso takoya haj salamatu ta tsaya takoya mata irinsu,
Amfani da abubuwan dake cikin toilet din gidan masu kudi,
Da hada shayi,
Da gyaran guri da sauransu.
Sannan sun siya mata kaya dai dai misali shidinma dan dai kada haj zeenah taganta da tsumman kayanta.
NAZLI kyakkyawar yarinyace fara tas me dogon gashi da dogon hanci gatada manyan idanu da dan lips dinta jajaye.
Duk da tana cikin tsananin wahala hakan bai hana tsananin kyawunta da nutsuwarta fitowaba.

TAFARU TAKARE
Karfe goma sha daya alh zaid umar ya iso kano da tawagarsa kai tsaye suka wuce babban masallacin jumaa dake kano dan acan xaa daura auren na dansa tilo dayake masifarso duk da dai angon bazai yiyu afito mutane dashiba yana can abj yabarosa.
Mijin haj salamatu alh yaro shi ne uban amarya wakilinta.
Guri yacika ya batse da manyan mutanen nigeria harma da jajayen fata jiniyoyine kawai ke tashi.
Karfe 'daya daidai dubban jamaa suka shaida daurin auren na
TAMEER ZAID OMAR DA NAZLI ADO TAKAI.

Tanajin alh yaro yashigo gidan yace andaura aure kuma ga jeep jeep nan guda goma alh ya aiko akai masu kai amarya airport suwuce abj.
Ido ladingo ta zaro tace ita wllh ba inda zata asallameta kudinta takomawarta gida taredasu

buba dasuka dauri auren.
Dubu dari hj slmt tabata suka wuce bayan nazli ta riketa tana sakin wani irin kuka maiban tausayi wanda har akaro nafarko da ladingo taji tausayinta amma tana duba gudin hannunta saita fincike tafice tana fadin,
ALLAH YASA YA 'DIRKO MIKI CIKI ACIKIN HAUKARSA.
Kuka take sosai mara sauti har suka isa aiport din itada hj slmt da jummai da wasu aminan hj salamatun.
Sam tashin hankalun datake ciki baibarta taji tsoron jirginba har suka isa abj wasu jibga jibgan motocin suka kuma daukarsu.

Wani hamshakin katon gida suka suka shiga mai hawa uku.
Haduwar gidan hartayi yawan fada ga masu tsaro zagaye da gidan.
A boys quaters aka saukesu yan aikin gidan suka dingi kawo musu abinci danasha.
Ruwa kawai tasha ta tsaya kallonsu iya jummai sunata kwasar gara.
Suna gamawa aka aiko haj nason ganinsu suka mike dukkaninsu suka bi bayan yar aikin.

Ya salam.
Falon dasuka shiga haduwarsa sam ta baci abd uwar dukiyar da aka narka acikinsa.
Zaune take akan daya daga cijin sofa din falon ta xuba ado tana baza kamshi.
Kallonsu tayi tace,
Tunda kun gama abunda yakawoku ga motanan yau komai dare xata kaiku kano.

Mint dun dubu daya ta mika musu tareda cewa su wuce idanda wani abu xata kira hj slmt a waya.
Mikewa sukayi jiki asanyaye suna mamakin wulakanci irin na hj zeenat din
Sun kawo mata 'ya amma ba godi bare nagode saima maidasu gida dazatayi adaren ko hutawa bazata bari suyiba.
Hj slmt ta kalli nazli tace,
Kiyi hkr nazli allah yabaki dauriya da hkr.
Suna ficewa ta fashe dasabon kuka dan ita gidan tsoro yake bata.

Kallonta dakyau hj zeenat tayi taga tayi yarinta amma aitunda andaura aure ai xata iyane tayi gyaran murya tareda cewa,
Kidaina wannan kukan dan bautar aure xakiyi idan kuma ya warke yasan yanda zaiyi da auren.amma dai yanxu kitashi akaiki part dinsa.ma'ana hawan karshe can ne part dinsa
Hawa na biyu kuma namu nida dad dinsa saina kasa gaba daya shine na baki da masu aiki.
Tameer baya iya mgn,
Baisan kowaba sbd kwakwalwarsa ta juye dan hk yanxu aikinki kulada cins,shansa,tsaftarsa da komaima nasa.
Nafeesa dauki akwatinta kikaita sama part din tameer kafin gobe taxo tagaida dad dinsa dan a goben xaikoma paris.

Stairs suka haye har hawa na karshe ta bude kofar falon dayafi na kasan tsaruwa da haduwa

tashiga har kofar dakin dayake cike takalli nazli tace,
Ni daganan xankoma kixo ki rufe muku falon dan yana fitowa idan akabar kofar abude.

Jikinta babu inda baya rawa amma haka ta rufe kofar falon hwy nabin fuskarta na tsoro da fargaba.
Hakanan taji tanason ta leka dakin taganshi taga ya yake.
Ahankali gabanta na faduwa ta tura kofar dakin ta leka.

Wani dan saurayin farin balarabe ta hango kwance a makeken gadon dakin yana bacci hnkl kwance kamar me cikakkiyar lafiya...

🌕🌕👉mamuh geee
🌕⚜️DA'IMAN⚜️🌕

NA

MAMUH GEEE

☆dedicated to☆
Husna bbchoudiallo

10→15

Saurin komawa tayi da baya tayi tareda jan kofar jikinta na makyarkyata fitsari na neman kufce mata tsabar tsoro
Sannan hawaye suka balle mata tayi saurin kuwa bakin kofar fita ta durkusa tana kuka tareda toshe baki dan kada kukan yafito.
'Kiyayyar dasu babah ladingo kemun harta kai su aurawa ajani ni dan wllh wannan ba mutum bane dan bantaba ganin mutum mekyau irin hakaba sannan gashi fari sosai yamafi 'dan megari dake birni karatu fari.

Kuka takara fashewa dashi rawar jikinta na tsananta.

Jin karar bude kofar datake tsugune ne yasa ta mike da sauri kamar fitsari zai zubo mata fuska cike tab da hawaye.
Wadda takowota dakince tadawo daukeda tray din abinci da magunguna takalleta taga yanda tayi shabe shabe da kuka da zufa duk da splite air con dake palon kusan guda uku batasan sanda tabushe da daria ba.
Ganin dariyar datakene yasa hankalin nazli yakara tashi takara barkewa da kuka.

Ganin dai da gaske take kukan ne yasa ta daina dariyar ta aje tray din akan center table din

palon takalli nazli duk saitaji tabata tausayi sbd kasancewarta yarinya amma sbd kwadayi iyayenta sun aurawa mai tabin hankali ita.

Yi shiru kidaina kuka ki fadi maiyasa kike kuka.
Jan numfashi tayi cikeda tsoro tace,

Tsoronsa nakeyi wlh bantaba ganin mutum mai kamarsaba.

Wata muguwar dariyace tazowa nafeesa amma saita gimtse sbd kada ta kara tsoratata akan wanda take ciki.

Kinga xo xauna nafada miki komai akansa.
Kasa xama tayi akan royal kushins dake palon sata sulale ta zauna akasa tana cigaba da shararar hawaye.

Itama nafisar akasa tazauna dan dama basa hawa kujerun gidan sbd zamansu yan aiki kuma hakan umarnin hajiyar gidanne wato haj zeenat.

Yaya sunanki?
Cikin muryar tausayi tace nazli.
To nazli zan fada miki komai gameda tameer dan yanda zakiji saukin fara dawainiyarsa.

Na farko abunda zan fada miki shine
Baya tashi bacci kullum sai karfe goma sbd allurar da dr yake zuwa kullum dare yana masa sbd yasamu yayi bacci dan idan bada alluraba baya bacci.

Abu nabiyu kuwa shine daya tashi zaki kama hannunsa kikai toilet kiyi masa brush kafin nan nikuma nakowo masa abincinsa saiki bashi kibashi magani daga nan sai masu yi masa wanka zasuzo suyi masa sai sauran aikin sa masa kaya nakine.

Atakaice dai sallarsa da cinsa da duk wani abun bukatarsa yana kanki.
Sannan babban abun shine ba'a barinsa shikadai adaki ko afalo ko a inama sbd tabin hankalin nasa mugun tsoro yasakar masa.

Kidainajin tsoronsa dan mutumne kamarki.
Abunda yasa kika ganshi haka mahaifiyarsace yar kasar larabawa
Dan haka ki kiyaye duk abinda kikaga baki saniba idan nashigi kawo abincinku kya sanar dani dan haj bataso yan aiki na hawowa sama saini kadai nima idan ba abinci xan kawoba bana hawowa.

Mikewa tayi da sauri ta fice sbd kada haj tafara kiranta bata kusa.

Wani irin wawan tagumi ta rabka tana juya bayanin nafisa a xuciyarta kafin tamike ta nufi dakin

dan kara lekawa taga balaraben.

⚜⚜⚜⚜⚜⚜

Ahankali yabude dara daran idanuwansa jin babu motsin akwai mutum adakin yasa yayi saurin xabura ya mike tsaye a tsakiyar gadon yana raba idanu.
Motsin shigowa dakin yaji aiko tsoronsa ya tsananta ya diro daga gadon da sauri yayi bayan kofar ya labe tareda saurin ciro durowar madubi ya lafe bayan kofar.

Ahankali kamar barauniya ta turo kofar tareda turo kanta aiko batayi auneba taji saukar abu kamar an kwada mata guduma ta dago idanuwanta dasuka fara ruwa ta dorasu akansa kafin ta sulale ta zube asume...

🌕🌕👉mamuh geee
🌕⚜DA'IMAN⚜🌕

Na
MAMUH GEEE

☆in dedication to☆
Husna bbchoudiallo

16→20

Ahankali suke saukowa daga stairs din hannuwansa makale da nata.
Gabantane ya fadi da karfi nan jikinta yafara rawa badan komaiba sai dan haj xeenat data gani hakimce a falon tana aiko musu da kallon,
Tsana,haushi dakuma mamaki dan idanda abundata tsana arayuwarta to tameer ne sbd son da mahaifinsa ke masa yasa takasa samun yanda takeso da tarin dukiyar ta alhajin.

Shima tameer na ganinta yayi saurin lafewa abayan nazli yana kara kankameta.

Cikeda izza tana yamutsa fuska tace,
Kifadamun ubanda yasaki sauko da wannan dan iskan mahaukacin nan inda nake baki.
Aminanta dasuke tare azaune palon ne suka bushe da daria 'dayar nacewa,
Wlh komai yafaru laifin kine zeenat dan babu yanda bamuyi dakeba akan kisan yanda kikayi aka turashi gidan mahaukata ki huta gaba daya amma kinki.

Cikin haushi tace,
Aike badan matsiyatan kudin danake tatsa a gurin ubansaba idan yana nan din da tuni na

gargadasa gaba sa gidan mahaukata.

Maida kallonta tayi kan nazli datayi wuki wuki tana sauraran makircinsu.
Tace,
Wuce munafuka matsiyaciya kuma wllh kinkusa barin gidannan dan naga alamar mahaukacinnan yafara sakewa dake nikuma ko acijin hauka banason nagansa cikin farin ciki.

Sum sum tajuya idanuwanta nakawo wasu irin hawayen tausayinsa.
Suna komawa a palo tazauna tana fidda hawaye masu ciwo sbd ganin allah sarki ita batada iyaye tanashan azabar babah ladingo sbd rashin gata.
Shikuma gashi da gata dajin dadin dunia amma anjuyarmai da kwakwalwa.
Saukar hannunsa taji afuskarta yana share mata hawaye wani sabon tausayinsa yataso mata takallesa cikin hawaye tace,
Nayima alkawarin jure duk wata wahala da barazana dazan fuskanta daga matarnan na tsaya na lura dakai har tsawon lokacin dazaka dauka kafin ka warke.
Kamar yasan abunda tafada sai kawai sakar mata murmushi tareda riko hannunta ya dora abakinsa tagane yunwa yakeji ta mike tareda bude fridge tadauko musu drink da biscuite
Da farko kin ci yayi amma ganin taci shima ya bude baki tafara bashi.
Suna gamawa suka zauna palon suna kallon tv wanda dagashi har ita babu mai fuskantar komai sbd shi dakeda ilimin yanxu beda amfani tunda kansa ya juye.
Itakuma bayan primary datayi Ikcin abbanta nada rai bata iya komaiba bare uban turancin da ake rerowa a tv.

Da tsakar dare tana kwance akasa kamar kullum saitaji kamar gadon da tameer din ke kwsnce na jijjiga
Tayi saurin tashi jikinta na bari saiko tagansa a kwance sai rawar sanyi yake har hakoransa na kukan haduwa da junansu.

Akidime ta dira gadon tana kiran sunansa yanajinta amma ko motsi baya iyayi takamoshi jikinta dukda yayi mata girma amma haka takamasa ta rungume tana sakin kuka ahankali dan gani take kamar mutuwa zai ita kuma ayanxu jinsa take kamar shikadaine dan uwanta.
Tun tana kuka har bacci yadaukesu ahaka basu saniba
Washe garima sai goma suka tashi.

Tun daga ranar takoma kwana akan gadon sbd kota kwanta akasa shima saukowa kasan yake ya kwanta kusa da ita kota lallashesa baya yadda yakoma.
Hakan yasa takoma gadon suna kwana atare.

⚜⚜⚜⚜⚜

Duk yanda haj xeenat ke tunanin shakuwarsu abun yawuce nan dan sunyi wata irin shakuwa.

Da gayya haj zeenat tadakatar da dr xuwa yana masa allurar dakesa sa bacci da dare wanda aranar dabaayiba sam basuyi bacciba yanata zabure xabure tana ganin hakan ta fashe da kuka tareda rungumesa tana cigaba da kuka.
Kamar wasa sai taga bacci yadaukesa
Tun daga ranar saita rungumosa jikinta suyi baccinsu hnkali kwance.
Kwanciyar hnkalin data samune da cima mai kyau yasa ta ciko kirar budurcinta ta bayyana ga wani kyawu da fatarta tayi.
Haka shima samun kulawa dayakeyi daga garetane yasa ya 'kara wani irin ja da kyau.

Yanxu ita ke masa wanka sbd duk masu hidimarsa haj zeenat ta dakatar dasu sbs acewarta nayi wahalar nikadai.
Sanin bashida hnkli baisan komai bane yasa nake sakewa muyo wanka atare ina saka ko wane irin kaya agabansa dan ganin baisan komaiba.

Much luv😘
AMINA JAJI
Daiman fan.

🌕🌕👉mamuh geee
🌕⚜️DA'IMAN⚜🌕

NA
MAMUH GEEE

☆in dedication to☆
Husna bbchoudiallo

21→25

Tadau fiyeda shekara agidan kuma acikin wannan shekarar abubuwa dasuka faru sune shakuwar dake tsakaninta dashi ta wuce tsammani wand hartakejin yazama wani 'bangare na rayuwarta datakejin bazata iya rayuwa babushi.
Jin tsananin sonsa take akowane second na rayuwarta.
Hutu da kwanciyar hankali yasa gaba daya ta canxa ta cika ta ko'ina dan yanxu taxama cikakkiyar budurwa.
Kiyayyar da haj xeenat keyiwa tameer gaba daya tadawo kanta soboda wata irin kaunsa da daddyn ya dora mata ga uwar dukiyar dayake kashe mata itada mahaukacin dansa shiyasa tadau mummunan kudiri akansu.
Xama suke kamar wasu makiya dan yanzu ko ruwa idan ba ita ta daukoba bata bari abawa

tameer dan hakama itake musu girkinsu akicin din palonsu.

Sannu ahankali har dad yasa aka kawo mai koya mata karatu agida tun bata ganewa hartafara ganewa hakama handbag dinta wato tameer duk inda tasa kafa ta dauke yana biye da ita.
Lokcin da dad yasiya mata mota yasa aka koya mata bata wani jimaba ta iya shiyasa yanxu har saukarsa take suje yawo sudawo abunsu.
Abu daya ta fara fuskanta yanxu akansa shine duk yaga anyi abu idan ya burgesa to sai ya gwada shima.
Duk yanda taso gason jin muryarsa bata samuba sbd haryanzu baitaba maganaba saidai taji sautin muryarsa lkc dayake daria idan suna wasa.

⚜⚜⚜⚜⚜

Sanye takeda doguwar riga wani shaking material dayayi masifar yi mata kyau tasanya dan karamin hijab tanata sauri ta gama ta sauka sbd malaminta yazo tun dazu.
Xaune ta taddasa a palon yakurawa tv ido yana kallo kamar idanuwansa zasu fado
Tasaki murmushi tarafa tafiya cikin san`da sbd tasamu taje ita kadai tunda hnklinsa yatafi a kallo kuma dama kotaje dashi makalkaleta yake ya hanasu karatun yanda yakamata.

Caraf taji anriko hannunta gabanta tayi mummunan faduwa sbd rikon baiyi kamadana tameer ba sbd shi makyalkyaleta yake.

Araxane tajuyo amma ga tarin mamakinta saitaga shine tsaye yarike hannunta din kuma riko mekyau sbd yanda takasa kwace hannnun.
Hankalinta bai tashiba saidataji yakai mata wata kyakkyawar runguma datasa numfashinta kusan daukewa sbd a iya saninta ta tameer baya rumgumarta saidai ya cukwuikuyeta.
Numfashinta taji yana fita da sauri ta zame da sauri tana dafa bango sai alokacin idonta yasauka akan tv taga wani romance film ne ake a tashar tayi sarin xuwa takashe tadan kallesa saitaga gabaki daya jikinsa amace yake.
Sum sum tawuce shikuwa akaro na farko yau baibita wani guriba.

Sam yau bata gane komai akaratunba hakadai aka tashi karatun takoma.
Kwance ta taddasa a palon yana ganinta yataso suka shiga bedroom tare ta aje littafanta suka koma palon nan da nan ta sake suka cigaba da wasarsu ta guje guje apalon kamar koyaushe.

🌕🌕🌕👉mamuh geee
🌕⚜DA'IMAN⚜🌕

Na

MAMUH GEEE

☆dedicated to☆
Husnah

31→35

Kashe gas din tayi ta fito kamar me satar hanya takoma daki ta zauna.

Har dare 'kin bari tayi su xauna guri daya.
Da daddarema haryayi bacci idonta biyu tana kallonsa dan ganin take idan tayi bacci wani abun kuma xaiti mata.

Da safe ma tun tana gudunsa harta daina sbd shi baimasan metakeyiba tunda ba wani hnkline dashiba.
Da maraice bayan sungama komai sun sauka gurin karatu ta lurada duk karatun datake idanuwansa nakan lips 'dinta datake motsawa
Duk saita fara rudewa sbd tsoron kada yayi mata kiss agaban malami
Aiko bata gama tunaniba taga fuskarsa ta nufo tata fuskar
Tayi zambur ta mike jikinta na rawa tana raba idanu.
Malamin yakalleta yanason tambayarta amma sai duk yaga a rude take.
Kafin yayi wata magana cikin sauri tace,
Mlm ina...ina..inajin ciwon kai abari sai gobe.
Da sauri ta wuce har 'kafafunta na hardewa.
Bin bayanta yayi shima da sauri suka shiga palo takama stairs ta haye.
Yanda take haye stairs 'din arude da saurine yasa ta taka ba daidaiba ta zame
Tameer dake biye da ita abaya ya ca'beta atsorace shima yana ware ido da le'ka saman yana duba wanda ya turota ta fado "danshi atunaninsa turota akayi.
Amma harya haye saman da ita baisaniba yanata ware idanu atsorace.

Kasa 'dauke idanunta tayi akansa tun lokacin daya tarbota harya 'dauketa ya hayo saman da ita.
Wani irin masifaffen sonsa takeji yana bin jinin jikinta tana kallon kyakkyawar fuskarsa har suka iso palon batasaniba saidataji yasaketa tim tafadi tsakiyar palon amma sam bataji zafiba saima binsa tayi da kallo tana murmushin dashi baimasan tanayiba.

Saidaya gama le'ke le'kensa kafin yazo gabanta data shagala da kallonsa duk inda ya wulga shima saiya saki murmushi ahankali yana kallon tsakiyar idanunta.

Ahankali ya taka ya isa gabanta har numfashinsu na haduwa sosai
Tayi saurin juya masa baya tana murmushi

Ya tsurawa bayanta ido yana kallon lafiyayyar fatarta fara tas data bayyana abu'dadden bayan rigarta sbd tuni gyalenta ya zame.
Wani kiss ya manna mata atsakiyar baya dayasata numfashinta sha'kewa tajiyo da sauri tana fidda numfashi da sauri da sauri
Bai tsaya komaiba ya kai bakinsa cikin nata yana bata wani mahaukacin kiss daya kashe jikinta takasa kwatace saima lafewa datayi ajikin nasa yana cigaba da kissing dinta.
Kamar wasa taji yana shafarta harda zura hannu arigarta amma sam takasa kwace kanta dan bakaramin kashe mata jiki yayiba.

Jin suna shirin xubewane yasa ta 'dan tattara 'karfin dabaifi cikin cokaliba ta xame tareda fadawa daki tashige toilet da sauri tana maida numfashi.

Da daddare bayan sunkwantama har bacci yafara 'daukarta taji yanata juyi ta bude idanu dakyar sbd bacci saitagansa ya dafe ciki yanata juye juye cikeda axaba ta tashi zaune da sauri takamosa arude tana kiran sunanta
Yana dude idanunsa akanta kawai saiya fixgota tafado jikinsa yana wani irin nishi yafara kissing dinta yana shafa arude takeso tashi amma sai maidata yake da karfi nan take wani irin tsoro yakamata tafara kuka tana kiran sunansa dan tasan tunda ba hankaline dashiba komai xai iya faruwa.
'Yar Rigar baccin dake jikinta ya 'barka da karfi yana lugwui gwuitata tako ina tana rixgar kuka duk karfinta amma sam kamar wani mai cikakkiyar lafiya sbd karfin dataji yanadashi.

Tanaji tana gani yakusanceta adaren
Yarabata da budurcinta ta dunkule gefe tana kuka awahalce sbd yanda ya nuna mata rashin tausayi sbd beda hnkali gashi ya kusance a lokacin baisan waye shiba itada taso saiya warke idan ya yadda ya karbeta amatsayin mata tukunna amma yanxu agaba idan yajita ba budurwaba yaki yadda da shine yakusanceta.
Duk ta tuno da hakan wani sabon kuka take saki sbd tsoron abunda xai iya faruwa agaba.

Shikuwa wani irin baccine yadaukesa cikin kwanciyar hankali yake sharar abunsa fuskarsa cikeda annuri.....

🌕🌕👉mamuh geee
🌕⚜️DA'IMAN⚜️🌕

Na

MAMUH GEEE

☆dedicated to☆
Husnah

41→45

Amai taketa she'kawa kaman ranta zai fita sbd babu komai acikin nata
Ga rashin 'karfin jiki.
Wanko bakinta tayi tana dafa bango radawo 'dakin tazaun 'kasa bakin gadon tana tsiyayar hawaye.

Motsi taga tameer nayi ta yunkura ta tashi ta isa kansa jikinta na rawa takira sunansa

Cikin rashin tsammani taga ya bude idanuwansa awahalce
Sbd ciwo dake cinsa

Ahankali kuma taga ya fara jijjiga idanunsa na juyewa

Ihu tasaki tareda dira kansa tana kuka mai karfi tana kiran sunansa.

Jitayi ya Shaketa da karfi
Idanuwanta suka firfito tana shure shure amma baida alamar sakinta
Shidewa take batunyi taji yasaketa yakoma yaxube kwance yana jijjiga jijiyoyin kansa duk sun fito ya ri'ke kan da hannuwansa yafara buga kan abango da karfi yana ihu..

Kuka tasaki tana tashi Duk da bata gama wartsakewaba daga muguwar sha'kar dayayi mata.

Hankali tashe take kallonsa kukanta na 'karuwa sbd ganin yana buga kan nasa sosai harya fara jiwa kansa
Da sauri ta isa ta 'kankameshi tana kiran sunansa cikin kuka

'Kokarin tureta yake daga jikinsa amma ta 'kankameshi ta'ki sakinsa sai kuka take.

Ahankali taji ya daina ya sulale 'kasa xaune idanuwansa arufe.
Xamewa tayi itama zaunen agabansa tana ta'ba fuskarsa datayi jajir tana jini tana hawaye tace,

Meer meyake damunka?
Meyasa ka chanxa sosai?
Pls meer kakoma yanda kake sbd zuciyata da kwakwalwata neman tarwatsewa suke,

Bansan yazanyiba.

Bu'de idanuwansa yayi sunyi jajir kamar bashiba ya 'dorasu akanta yana kallonta awahalce.

Tana ganin yabude ido ta mi'ke da sauri ta dauko 'dan 'karamin towel da ruwan 'dumi tafara goge masa jinin fuskarsa tana tanajin ra'da'din ganinsa ahaka.

Idonsa akan fuskarta ko 'kyaftawa bayayi ahaka ta goge fuskar ta mike ta maida kayan tazo tashiga toilet ta ha'da masa ruwan zafi a bathtub ta fito takamasa takaisa har cikin ruwan.

Suna fitowa ta zaunar dashi ta goge masa jiki tasakamai kayan shan iska tazaunar dashi ta fice zuwa 'kasa dan samo masa abinci.

Abincin aikinta takarbo takawo masa dakyar ta lallabasa yaci sbd jikinsa da yayi xafi sosai alamar xaxxabi.

Kwantar dashi tayi ta lullubesa takoma gefe tana kallon sauran abincin tanajin yunwa amma baxataci ba sbd kada yatashi babu abunda zaici duk da darene.

Da wuri ta tashi tayi sallah tana idarwa shima yatashi takaisa toilet sukadawo tasashi yayi sallah yana idarwa wani sabon xaxxabin yataso masa tamayardashi gado ta futa zuwa aiki.

⚜⚜⚜⚜⚜

Gaba 'daya rayuwar ta juye mata
Da kuka take yini,
Da kuka take kwana,
Sbd komai ya lalace mata
Tameer gaba 'daya baida lafiya
Ga doke doke dayake wani lokacin yayita farfasa kaya
Idan kuwa ya damketa saita kusa mutuwa allah ke kubutar da ita.
Wani lokacin har falla mata mari yake bakinta yayita jini.
Idn kuma haukar ta kwanta to kwana yake cikin matsanancin xaxxabi..

🌕🌕👉mamuh geee
🌕⚜️DA'IMAN⚜🌕

Na

MAMUH GEEE

☆dedicated to☆
Husnah bbchoudiallo

46→50

Ta rame sosai tayi wani irin haske wanda takesa ran 'kila jinine babu ajikinta
Ta fige,ta hargitse sbd wahala da yunwa ga tashin hnkalin tameer da yanxu gaba 'daya tsoronsa take dan yanda alamun cikar hauka keta bayyana ataredashi.

Shi kansa tameer yayi wata irin muguwar rama sbd yanxu gaba 'daya ko abinci baya iyaci kota basa
Rayuwar ta ida birkice masa gabaki 'daya.

Aikin bawa flower ruwa taketa famanyi
Sai sauri take tagama sbd mugun jirin datakeji duk da bawani kuzari takedashiba sbd tuni tayi hannun riga da lafiya.

Batayi auneba taji Jiri mai 'karfi ya kwasheta ta xube abun ban ruwan dake hannunta yayi sama yadawo mata ruwan dake cukinsa suka xube ajikinta gaba 'daya.

Sanyin ruwan yashigeta sosai ga muguwar buguwar da kanta yayi.

Goge hawayenta tayi tareda daddafawa ta mi'ke tana kallon kayanta dasuka jike ta nufi babban palon dan xuwa sama ta chanxo kaya.

Tana shiga palon ta du'kar da kai sbd haj xeenat na palon hakimce tana waya.

Hanyar hayewa stair ta nufa tana kakkama jikinta sbd sanyin A.C daya ciki palon gata kuma kayanta ajike.

Wani razanannen ihu taji haj xeenat tasaki ta juyo da sauri har jikinta na mazari.

Nafisa ma dake kicin aguje ta fito hartana zamewa a tiles.

Fizgo nazli tayi da wani irin mugun 'karfi dan yanda tashin hnkali da ki'dima sukasa idanuwanta rufewa
Wannu ta 'dora akai tana kallon rigar yadin dake jikin nazli ta kwanta ajikinta sbd ruwa ta nuna cikin nazli jikinta na rawa murya asar'ke tace,

Me..me..mene..ne wannan?

Nazli da nafisa atare suka kai kallonsu ga kallon cikin nazli suka ga ya'dan taso ka'dan

Nafisa data fahimci me haj xeenat ke nufi itama ta waro idanu cikin kidima da tashin hnkali.

Nazli kallon cikinta take tanason taga abunda ya 'daga musu hankali amma bata ganiba bayan cikinta daya kumbura kadan wanda take tunanin yunwace ta kumburar mata dashi dan tuni ta lura da kumburinsa.

Figitaccen marin da haj xeenat tasakar matane yadawo da ita  hnklinta kafin ta wartsake marin takuma xabga mata wani wanda ya haddasawa hancinta 'barewa da jini.

Rufeta tayi da duka kamar mahaukaciya cikin tashin hnkli kaman zatayi kuka take fadin,

Wllh kasheki zanyi,
Bazan bari wannan abun yafaruba koda zanyi yawo a tsirara,
Bazan taba bari haka tafaru ba,
Allah ya isa tsakanina dake shegiya munafukar karuwa.

Ganin haj bata hayyacinta gaba 'daya yasa nafisa doka shahada tayi kukan kurar 'kwace nazli tana bawa haj hakuri

Zaman 'yan bori haj xeenat tayi bakinta na kumfar fitina da masifar tashin hnkli.

Dakyar taja jiki ta tashi daga kwancen tana hawaye hancinta da bakinta suna fidda jini
Sai kakkarwa jikinta yake dan bakaramin duka haj xeenat tayi mata ba ga mararta dataji ta

'daure nan take ta dafe ciki tana tsiyayar wasu hawayen.

Rarrafe take kokarinyi ta haye sama tsabar wahala

Haj xeenat ta xabura tsaye tayi kanta ta shakurota tajawota kamar kayan wanki ta dawo da ita tsakiyar palon ta wurgar tareda rarumo wayarta jikinta na rawa takira dr tace maza maza yazo yanxu tana son ganinsa..

🌕🌕👉mamuh geee
🌕⚜️DA'IMAN⚜🌕

Na

MAMUH GEEE

☆dedicated to☆
Husnah bbchoudiallo

51→55

Kafin dr ya iso kasa zama tayi tafara safa da marwa afalon tana jin xuciyarta kaman xatayi bindiga ta fashe.

Baiwar allah nazli kuwa tuni azaba da zazzabi mai mugun 'karfi ya dirar mata jikinta babu inda baya karkarwa sai hawaye take tsayayarwa dan har alokacin batasan abunda haj xeenat ke nufiba.

Minti goma sha biyar saiga dr yashigo palon
Haj xeenat tayo kansa tana nuna nazli da hannu tace,
Dr dubamun yarinyarnan dan banason xargina akanta ya tabbata.

Shima cikeda mamaki yakalli nazli 'din dakyau na tsawon lukuta
Tabbas amatsayinsa na dr yaga wasu lamomin ciki atattare da ita tunkan ya duba
Amma dandai su tabbatar yamatso gabanta ya dukusa yayi mata wasu yan tambayoyi amma ko magana takasayi sbd matsanancin halinda take ciki.

Roba yaba nafeesa yace,
Kamata kuje toilet inason fitsarinta yanzu.

Hannu biyu nafisa tasa takamata sukaje toilet 'din 'dakin nafisa dake palon.

Suna dawowa nafisa ta mi'ka masa ya karba da hannuwansa daje cikin hnd gloves ya fiddo da pt strip yasaka cikin fitsarin ya dangwalo ya rike yana kallo dan ganin abunda result zai bayar.

Duk wani numfashin haj xeenat dake fita dakyar to 'daukeda tashin hnkli da tsoro yake fitowa
Sai addua take allah yasa kada result 'din ya nuna positive.

Ko 'kyafta idanunta batayi daga kan pt strip 'din
yawuma dakyar take hadiyesu.

POSITIVE shine abunda result ya nuna

Kawai sai hawaye suka gani a fuskar haj xeenat ta mike kamar guguwa tayi 'dakinta
Ta fito da damin kudi ta xubewa dr tana cewa,

Gasunan idanma basuyiba xan 'karama koma nawane KACIREMUN SHEGEN CIKIN JIKINTA AYAU BASAI GOBEBA.

Nazli dr nafisa atare suka mike tsaye sbd tsoro da bazatar furucinta
Hardai nazli da furucin na haj yasa ta fahimci abunda tun farko haj ke nufi harta kira dr kuma ya tabbatar da cikine da ita har takeson axubar.

Bata taba saran zata iya mikewaba sbd axabobin ciwon datakeji acikin jikinta
Amma ta zabura ta mike cikin tashin hankaki biyu
Dana jin tana 'daukeda ciki dakuma jin xa'a xubar mata dashi.

Magana dr xaiyi ta 'daga masa hannu fuska adaure tace,

Deal ne xakayi kona nemi wani?

Damin Kudaden yakalla yaji bazai iya bari suwucesa suje gurin waniba
Koba komai idanma baiyi ya tabbatarda saitayi tunda tayi niyya.

Tattara kudin yayi yana xubawa ajakar kayan aikinsa dayazo da ita yana cewa,

Nafisa kamata kusameni amota muje asibiti yanxu na wankosa waje.

Ajiyar xuciya haj xeenat tasaki tana wani shu'umin murmushi.

Kamar wata rakumi da akala takoma tanajin wani radadi daya danne zuciyarta
Takasa bude baki tayi magana sai hawaye dake gudu a fuskarta nafisa tajata suka tafi.

Bushewa xuciyarta tayi dan itama gwara acire mata cikin dan batason ta haifosa yaxo ya tarar da wulakantattar rayuwar dasuke ciki itada mahaifinsa kuma batada tabbacin idan yazo duniya ubansa xai karbesa idan ya warke.

Tunani mai xurfi nafisa tashiga tanajin bazata iya bari axubar da magajin wannan babban familyn me tarin dukiya ba
Amma tana tsoron yiwa dr magana yakoma yafadawa haj.

Har suka kai asibitin suka 'dunguma xuwa office 'dinsa suka xauna shikuwa kasa xama yayi yafara kai kawo yana tunanin
Tabbas idan yazubar da cikin jikan alh zaid to yaxama cikakken maha'inci kuma butultacce sbd alh xaid ne sanadin duk wani matsayi dayake akai yanxu
Afterall yafi kowa sanin alh zaid da tameer suna tsananin bukatar 'da jafin duk ashiga cikin wannan halin na ciwon tameer.

Dakewa nafisa tayi ta mike taje gabansa ta tsaya takallesa cikin ido tace,
Idan xuciyarka batason yi kada kayi
Kuma ka tuna komai daren dadewa gaskia xata iya bayyana alokacin da baka tunani.
Shin me xamu samu idan muka cutatar da rayuwar wa'inda suka taimaki rayukanmu suka kyautata rayuwarmu.
Dan allah inason kayi amfani da shawarar da zuciyarka ke baka kadaka cutatar da cikin nan🙏

🌕🌕👉mamuh geee
🌕⚜️DA'IMAN⚜🌕

Na

MAMUH GEEE

☆dedicated to☆
Husnah bbchoudiallo

56→60

Kallon nafisa yayi yana nazarin kalamanta kuma sun shigesa sosai ya zauna tareda huro iska Yace,
Tabbas bazan iyaba sbd alh da tameer bazan iya cutatar da gudan jinin suba
To amma kobanyiba haj bazata zaunaba saita tabbatarda babu cikin nan kuma yanxu bama cikin kadaiba tunda harta gane tameer zai iyayin ciki ayanayin dayake ciki to tabbas zata 'dauki mummunan mataki akan hakan.

Kukan nazli ne ya tsaidasu sbd kukane take rerowa mai ciwo daban tausayi sbd ganin yanda rayuwarta takoma dakuma rayuwar abundake cikinta tun baizo duniyaba.
Durkusawa tayi gaban dr tana tsiyayar hawaye tace,
Idan har halaccin da daddy yayima kakeson mayarwa to
Dan allah kakiramunshi yasan halinda 'dansa yake ciki,
Meer yana cikin tsananin halinda yake bukatar taimako
Amma babu mai taimaka masa,
Dan allah ka taimaka kakirasa koxata shiga.

Duk yanda sukaso su samu daddyn basu samesaba har suka gaji.

Kallonsu yayi bayan yayi scanning 'din cikin yafara musu bayani,
Yanzu zan baki maganin karin jini saiku fadawa haj anxubar da cikin
Illa dai abu 'daya dazan fada muku shine kushirya tarbon tashin hnklin dazai biyo baya idan cikin ya fito gaba 'daya
Dan ni nanda sati mai xuwa zanbar 'kasar zuwa wani aiki.

Babu me cikakkiyar nutsuwa suka dawo gidan sbd gudun kadata gane.
Tana ganinsu tasaki murmushin 'keta dajin 'dadi tareda jinjinawa dr.
Shikuwa bai tsaya dogan zanceba yatafiyarsa dan gaskia yana shakkar haj zeenat sbd rashin

imaninta.

Har 'palonsu nafisa takaita tasauko cikin tunanin bala'in dazai nufatosu nan gaba idan haj xeenat tagano gaskia.

Kwance ta tarar dashi idonsa biyu yabita da kallo da kyawawan idanunsa batasan sanda taje da gudu ta fada jikinsaba tareda sakin 'dan siririn kukan tausayinsu dakuma wani jarababben sonsa datakeji dakuma cikin jikinta daya kasance tsotsonsane.

Shima rungumeta yayi yana lumshe ido akaro na farko taji yace mata,
Shihhhhhh.

Cikin farinciki da hawaye ta 'dago tana murmushin datama manta ya ake yinsa ta 'kara 'kankameshi tanajin sonsa.

Wanka sukayo sukayi sallah tare sukaci abincinta na aiki.
Mikewa tayi zata fita yayi saurin dawo da ita jikinsa yana kallon 'dan bakinta
Batai auneba taji nasa bakin anata yana bata wani irin kiss me dadi.

Sam batayi yunkurin kwacewaba harya fara shafarta yana zura hannuwansa cikin rigarta nandanan yafice hayyacinsa ya sureta sai gado.

Sosai suka raya daren wanda rabonsu da zama ma kusada juna harta manta bare wata soyayya.

Tund safe cikin bacci taji ana 'barin kaya
Ta tashi afirgice
Idanuwanta suka sauka kan 'dakin
Ya fasa komai na 'dakin ya hargitsashi ta hango jini akasa da sauri ta diro gadon jikinta na 'bari ta xari riga tasaka tayi palon a tsorace aiko komai na palon ya fasa duk yajiwa kansa rauni sbd hannuwansa jini suke fitarwa sosai ga 'kafafunsama haka.

Juyowa yayi suna hada ido ta ha'diyi wani yawu da 'kyar sbd gaba daya kamannunsa sun chanxa idanuwansa sun birkice
Tafara 'kokarin ja da baya dan ganin ya nufota.
Cikin rashin sa'a ta taka kwalba cikin abubuwan daya fasa ta fadi 'kasa aiko nan yahau jibgarta da 'kafa yana taka kanta
Tun tana motsi harta daina ta sume agurin.

🌕🌕👉mamuh geee

🌕⚜️DA'IMAN⚜️🌕

Na

MAMUH GEEE

☆dedicated to☆
Husnah bbchoudiallo

71→75

Tapia suke ta 'kankame hannunsa tana waige waige jikinta sai 'bari yake har lokacin ga mugun zazzabi tanaji
Shi kansa tameer ciwone ajikinsa sosai dan layi kawai yakeyi idanuwansa a lumshe.

Tafia kawai suke batareda tasan inda suka dosaba
Babban tashin hankalinta baifi dataga dare yafara tsala musuba ga tameer daya fara ficewa hayyacinsa yana 'kokarin xube mataba ga jakar kayansu haka itama ta galabaitu matuka.

Wata motace ta 'dan tsaya gabansu
razana tayi tareda ja da baya tana 'kankame tameer.

Wani wurjigegen inyamuri tagani cikin motar yace,
Madam do you need a taxi?

Kallonsa tayi cikin tsananin tsoro tana hada gumi
Kafin tabasa amsa sukaga tameer ya sulale agurin.

Sakin jakar hannunta tayi aki'dime ta cakumosa tana kwala kiransa.
Idansa ya'dan bude awahalce akalleta yamaidasu ya lumshe.

Da sauri ta bude motar tana kokarin tadashi jiki na rawa
Direban ganin yanda take kiciniyar kamasa duk a rude takasa ya fito ya kama matashi suka sakashi cikin motar yasaka musu jakarsu tareda shiga motar yace ina zai kaisu?
Shiru tayi tana hango tashin hnkalin dazata tadda amma bayanda ta iya dole can xata kodan ganin tun yanxu sun fara yagayyara ga tameer na.....

"Kano. Tafada murya na rawa hawaye na silalowa daga idonta ahankali.

Direban kallonta yayi ta mirrow tareda maimaita kano cikin wawuyar hausarsa kafin ya girgixa kai ya tada motar da nufin kaita tasha tunda yasan shidai ba kanon zashiba.

Har aka kai tashar bata hayyacinta sbd hawayen daketa zirarowa daga idanunta tana kallon fuskar tameer dake nuna yana cikin tsantsar ciwo.

Suna isa tashar ya suka fito ya karbi dubu daya yatafiyarsa.

Duk da darene amma akwai mutane sosai atashar sunata sha'anin gabansu.
Rabewa sukayi bakin wata rumfa atsorace take gaba 'daya banda kuka ba abunda take.

Tana kallo ahankali bacci mara da'di ya'dau tameer.ta cusa kanta tsakiyar gwiwowinta tana rero kukan tausayinsa san gwara ita tasaba da wahala amma shi baisan wata wahalar rayuwa ko 'dayaba
Gashi yanxu batasan wace irin rayuwa zasuyi ataredasu babah ladingo.

⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜

NAZLI ADO BUBA TAKAI shine sunanta,
Mahaifinta adamu abubakar 'dan asalin takai ne kuma maraya daya taso hannun kakarsa dan yarasa iyayensa tun yana yaro.
Yayi karatu dai dai misali dan headmaster ne primary school 'din 'yan 'kauyen.
Matarsa 'daya ladidi wadda ake kira da babah ladingo
Da 'ya'ya biyu bubah wanda yaci sunan headmaster malam ado,sai idi.

Daga ladingo har 'ya'yanta babu me hali na kirki ko mutunci.
Sam su bubah banda sace sace da 'kwaya basusan komaiba wanda ladingo ita ta lalata abunta danko malam bai isa yayi maganaba akansu.

Raihanat budurwar buzayen nijar dasukayi gobara suka rasa dukiyoyinsu da gidajensu ta rasa iyayenta sai aminin mahaifinta 'dan uwan me gari dashima acan yake kuma yayi basa rashin saiyazo da ita tareda matarsa da 'yarsa 'daya asmah ya hadasu ya rike.

Basu wani jimaba agarin ya aurar dasu
Ita raihanat ga headmaster ado dake sonta sosai sai ita asmah acan 'kauyen gaba dasu ga wani 'dan dagacin 'kauyen.

Bayan aurensu da wata biyar allah yakarbi ransa me 'dakinsa ta tattara ta tafiyarta garinsu

itama.

Raihanat dai takoma batada kowa sai mijinta wanda gaba 'daya rayuwar gidan sam batada da'di ko kwanciyar hankali dan ladingo da 'ya'yanta sun saka gaba da tsangwama ga cuta iri iri gefe 'daya ga aminiyar ladingo wato iya jummai da kullum tana gidan suna cutatar da ita.
Iya jummai mijinta ya jima da rasuwa sbd ba'kin cikinta dana 'yayanta iro da karima.

Raihanat nada hakuri da biyayya sosai shiyasa mijinta ke tsananin sonta dan agurintane kawai yakeji sanyi.
Ahaka ta haifi 'yarta ta fari nazli mai kama da ita sosai sak buzuwa.
Haka 'yarta girma babu ranar dazasuce sunyi farin ciki a rayuwarsu ta gidan sai gashi garin haihuwa ta biyu su ladingo suka rufeta a'daki tana nakuda tayita neman taimako tana rokonsu amma suka 'ki budeta saida suka tabbatar da axaba ya kasheta.

🌕🌕👉mamuh geee
🌕⚜️DA'IMAN⚜🌕

Na

MAMUH GEEE

☆dedicated to☆
Husnah bbchoudiallo

66→70

Zaune take bakin gadon dayake kwance tana shafa lallausan gashin kansa dake kan cinyarta ahankali idonta akan fuskarshi tana kallo shima ita yake kallo yana lumshe idanun marasa lpia.
Gabanta ke'dan faduwa akai akai dan haka takasa tashi tabar gurinsa.

Hawayene suka gangaro daga idonta ahankali suka sauka akan fuskarsa
Ya rintse ido sbd jin afuskarsa suka xuba amma a xuciyarsa yaji zafinsu.

Hannu ya 'dago yana rawa ya shafo fuskarta tareda girgiza mata kai alamar ta daina kuka.
'Karasa rushewa tayi da kukan ahankali tana cewa,
Meer inajin wani irin nauyi a xuciyata dana kasa ganewa,
Meer idan narasaka bansan ya rayuwata xata komaba,
Pls meer kada katafi kabarni,
Kabari na rayu dakai dan rasaka daidai yakeda tabarbarewar rayuwata.
Meyasa nakeji kamar wata rana xaka barni?
Meer pls dnt ever leave me sbd kaine rayuwata da abunda zan haifa.

Yanda take kukan ne tana maganganun yasa ya tashi zaune dakyar tareda jawota jikinsa ya rungume tsam.

Saidata sha kuka sosai har kukan baya fita kafin tafara sauke ajiyar zuciya ahankali har bacci ya 'dauketa.

⚜⚜⚜⚜⚜⚜

Kaida kawo take a tsakiyar makeken 'dakinta.
Xuciyarta a cunkushe take ta rasa gasgata abunda xuciyarta da shawarar aminanta suke bata.

Ingizata xuciyarta takeyi akan tayi gaggawar aikatarda 'kudirinta akansu.

Zama tayi bakin gado tareda 'bata fuska tana cewa,
To idan nakoresu ai zasu iya dawowa wata rana hardai idan shegen balaraben yaron nan ya warke.

Zabura tayi tana cewa bazai yiyuba.

Wayarta ta 'dauka rai abace ta nemo wata number takira tana huci.

Ringin biyu wayar tayi aka 'dauka
Cikin 'kosawa tace,
Lilo ya alhajin yake?
Lpia klau haj saidai ciwonsa gaba yake.
Kyalesa indai kuna basa abinci.
Yanxu dai akwai aiki na musamman daxakuyi a daren yau.
So nake kuzo da daddare inason ku aika mahaukacin 'dansa barxahu tareda shegiyar aljanar matarsa kuma banaso asamu matsala.
Angama haj kawai yanxu naji alert.

'Kokarin sakin tray 'din hannunta take nafisa tayi saurin tarewa tana zare idanu tareda ha'de wani wahalallen yawu tana dam'ko hannun nazli sukabar 'kofar 'dakin sbd datayi 'barin kayan to tabbas data jawo musu masifar datafi wadda sukaji.

Kicin suka koma ko wanne jikinsa na 'bari tsabar tashin hnkl
Nazli ta saki wani irin kuka tana sulalewa 'kasa
Nafisa ma tsabar rudu kukan take dan iya ka'duwa ta ka'du da abunda sukaji haj na fa'da.

Kuka take mara sauti sosai kamar ranta xai fita
Jikinta har karkarwa yake tana sha'kewa.

Cikin tsananin tausayi nafisa ta dafata murya na rawa tace,
Na..na..nazli inaga kija sir tameer ku gudu wani guri nesa da inda bazata taba sanin kuna canba,
Nazli yanxu kece komaina sir tameer tunda mahaifinsa babu labarinsa,
Kodan kasancewarsa UBAN 'DAN DAKE KWANCE ACIKINKI.

'Daki taje da sauri tadawo rikeda kudi masu 'dan afki ta kamo hannun nazli ta dam'ka mata su tana hawaye tace,
Ki tafi dashi nazli,i trust you,
Nasan ke kadaice xaki kula dashi fiyeda kanki.

Tayar da ita tayi jiri na 'dibarta tana sheshshekar kuka suka hay stairs 'din takaita har 'kofar palonsu ta juya.

Gadon dayake kwance yana bacci ta nufa tana toshe baki sbd kukanta dayake tsananta
Ta xube akansa tana sakin kukan gaba 'daya.

Sosai ta risga kuka cikeda tausayin ya rayuwarsu zata koma idan sukabar gidan,
Ya zatayi da tameer daba lafiyane dashiba.
Ina suka dosa?
Yazatayi da kanta,tameer dakuma abunda ke cikinta.

Kiran sallar magrib yasata ta mike tana goge hawayenta tareda fa'dawa toilet tayo alwala tayi sallah
Ta tadashi takaisa yayo alwala yayi sallah.

Kayansu ta zuba a akwati 'daya tana danne kukanta ta kama hannunsa tana kallon 'dakin hawaye nabin fuskarta tajasa suka fice gidan batareda kowa yaga fitarsuba danko masu gadi suna cikin masallacin gidan suna sallah..

🌕🌕👉 mamuh geee
🌕⚜️DA'IMAN⚜🌕

Na

MAMUH GEEE

☆dedicated to☆
Husnah bbchoudiallo

76→80

Rayuwar nazli ta tagayyare danko wanka ladingo bata iya yi mata sai idan malam da kansa yayi mata dan ya'dauki son duniya ya 'dora ga 'yarsa nazli.
Tana isa sakawa makaranta yasakata duk zashi aiki tare suke zuwa su dawo tare ahaka harta girma tasan kanta tanada shekara goma sha 'daya ya rasu yabarta cikin muguwar ukubar ladingo.
Ta taso cikin wahala da azaba.
Duk wani aikin gidan ita keyinsa,
Ga sana'ar abincin ladingo itake 'dorawa duk da aikin yafi 'karfinta kuma idan tayi ba daidaiba a aikin buba ko idi take sawa ko iro 'dan iya jummai su laka'da mata dukan da saita gagara motsa koda 'dan yatsanta.

A mataccen 'dakin mahaifiyarta take zama bayan duk sun kwashe tarkacen kayan 'dakin suka barta da 'yar matacciyar tabarma ga 'kofar 'dakikn sun cire.
Ahaka ta rayu ta girma acikinsu har wannan auren 'kaddarar yahau kanta.

⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜

TAMEER ZAID OMAR
Alh zaid omar 'dan asalin jahar maidugurine.
Yanada tarin dukiya mai 'dinbin yawa wadda ya gada ga iyayensa dakuma 'karin tashi daya tara takansa.
Alh zaid omar su biyu kacal iyayensu suka haifa kafin su rasu shida yayarsa dayafi so fiyeda komai wato HAJ NURATU.
Haj nuratu nason 'dan uwanta itama fiyeda komai wanda duk wandake tare da ita zai sheda hakan.
Haj nuratu na aure a 'kasar cairo sbd mahaifin mijinta alh kabeer balaraben can ne sai mahaifiyarsa yar maiduguri.

Zamanta acan yasa shima alh zaid yamaida rabin business 'dinsa acan.
'Yayan haj nurat biyu isma'il da ammar.

Ganin da gaske alh zaid baida niyyar aure yasa tasakashi agaba harda hawayenta akan lallai sai yayi aure
Hankalinsa ya tashi sosai ganin yayarsa na hawaye
Ya lallasheta tareda bata zabin matarda taga ta dace dashi.
Farin ciki tayi sosai dan dama akwai 'yar 'kanwar surukinta datayi masa sha'awarta balarabiyar asalin cairo 'din mai suna NYSSA.

Bawani dogon zancen suka amince da juna haka iyayenta basuyi jaba sbd sunason nurat kuma suna yaba halayenta dan haka sunsan 'kaninta xaiyi kirki kamarta.

Aurensu da shekara bakwai nyssa ta haifi 'danta namiji balabe sak ga tsantsar kyawu
Aka saka masa suna tameer.

Soyayya da gatan da tameer yake samu ba ka'dan bane sbd takowane 'bangare kowa sonsa yake bama kamar iyayensa da haj nurat dakejinsa fiyeda 'yayanta
Ga 'bangaren dangin nyssa masu tashen dukiya mai 'dibbin yawa agarin suma tsananin 'kaunarsa suke.
Haka ya girma a sangarce harsaida yayi shekara goma sha biyar kafin mum  'dinsa takara haihuwar mace taci sunan FANNAH.

Tsabar dukiyar alh zaid yasa yayi suna sosai ako ina wanda gidan tashar gatanmu channel dake kaduna nigeria ta aiko da ma'aikatanta na musamman dan samun ganawa dashi.

Ranar daya gana dasu ma'aikatan nakomawa masaukinsu xeenat takasa zama saikai kawo take tanajin wani irin kwa'dayi da son alh zaid yayi mata dirar bomb axuciya wanda daga 'karshe ta 'dau mummunan 'kudiri akansa.

Kodata dawo nigeria gidan aminiyarta haj kareema ta nufa ta fesa mata aiko nan suka 'dunguma gidan abokiyar cin mushensu haj bilki daganan suka 'dunguma gurin boka.

Bayan uwar dukiyar dasuka kashe aikinsu yafaraci dan kuwa tana kiran wayarsa kiran farko daya 'dauka tafara masa bayanin kanta ya datse kiran sai gashi bayan kwana biyu dakansa yakirata.

Sannu sannu aiki yafaraci saiga alh zaid harda zuwa nigeria gurin xeenat inda anan ne sukayi aikinsu na 'karshe akansa wanda baikomaba saida aurenta akansa.

Dukiya da daular daya sakar matane yasa nanda nan ta chanxa tazama hamshakiyar haj dan dama can ba yarinya bace ta'dan kwana biyu.

Dunia tadawo musu sabuwa itada aminanta da mahaifiyarta Haj sabuwa da itama boss ce harkar bin bokayen kafin mijinta ya yarasu.

CAIRO
Sannu ahankali suka fara ganin chanji daga alh zaid dan yanxu akai akai yake xuwa nigeria kuma yakan jima acan.
Tsananin son dayakewa matarsa da 'dansa harma da 'yar uwarsa bai rageba shiyasa basu kawo komaiba arai sai tunanin kila business dinsane.

🌕🌕👉mamuh geee
🌕⚜️DA'IMAN⚜🌕

Na

MAMUH GEEE

☆dedicated to☆
Husnah bbchoudiallo

81→85

Ganin daular da haj xeenat take cikine yasa suka 'kulla 'kullalliyarsu suka aika mijin haj bilki barzahu ta aure mijin 'yayar wata 'kawarsu gurin aiki mai tarin dukiya shima dake abuja bayan sun kore matarsa daga gidan.

Haj kareema ma wani minister ta aura bayan ta tarwatsa matarsa da 'yayansa ya koresu ta haifi 'yarta meenah
Wadda sam batada tarbiya ko kadan.

Ganin haryanxu yanason matarsane yasa haj zeenat yanke shawarar xuwa harcan ta tarwatsa zaman tunda anyi aikin har angaji yakasa ciresu aransa koda da minti 'dayane.

Tana isa cairo kai tsaye gidan yayarsa tafara isa cikin iko da takama.

Zaunawa tayi tana murmushin 'keta saiga haj nurat 'din tafito sbd ansanar da ita tanada bakuwa.

Kallon mamaki takebin xeenat dashi kafin tadan saki fuska tana mata sannu suka gaisa aka kawo mata drinks.
Ruwan sanyi ta kurba tareda crossing legs tana girgixawa tace,
Sunana haj xeenat zaid omar.

Kallonta haj nurat tayi dakyau amma bataga alamun hauka atareda itaba saita 'dan saki murmushin ya'ke tace,
Allah sarki wane zaid omar 'din?

Zaid omar 'kaninki
Ni matarsane tsawon shekara uku kenan ina zaune a abuja nigeria.

'Kuri tayiwa haj xeenat tanason tayi tunani 'kwakwalwarta takasa dan ita takasa ma tuno me xeenat 'din tace tsabar rudani.

Kafin tace wani abu saiga alh zaid sun shigo shida matarsa dasu tameer
Tasaki ajiyar zuciya tana kallonsa dan bakaramin dadin ganinsa tayiba alokacin.

Idanunwansa na sauka kan xeenat ya washe baki duk da ya razana sosai da ganinta.

Ganin yanda yasaki fara'a be yasa suka kalli juna cikeda mamaki.
Haj nurat ta'dan ha'de fuska tace,
Zauna ka fadama wacece ita.

Zama yayi yana kallon fuskar nyssa dan makaramin so yake mataba
Yamaida kallonsa ga yayarsa murya a'dan tsarge yace,
Kuyi hakuri naso na bayyana mukune yanda xaku fahinta amma kuma sai abun yazo ahaka
Xeenat matata ce,
Munyi aure shekara uku yanxu.

Kallonsa suke dakyau ba alamar wasa axancensa bari makamancin hakan.

Iya 'kuluwa sun 'kulu
Nyssa ta mike tareda sa'ba fannah akafada ta fice afalon batareda ko gefensa ta sake kalloba.
Haj nurat ma mikewa tayi tashigewarta tabarsu.

Mikewa yayi yabi bayanta ta dakata da tafiya ta juyo ba 'bata lkc tace,
Tabbas bani bakai idan har kana tareda waccar matar.

Zaro ido haj zeenat tayi dan tana labe tana jinsu.

Lallai zanyi maganin wannan matar tafada tana 'kafa.

Tashin hnkli akayi sosai amma aikin asiri yaki bari yasaketa ga nyssa tuni tafara ciwo sbd mugun 'kullin da haj xeenat tazo dashi ta barbada mata a palo sbd 'karfi da yaji suke zaune gida 'daya.

Tameer bayanan yana paris karatu
Kwanciyar hankali ta 'kauracewa familyn dan nyssa ciwo ya munana ga xeenat taki komawa
Shikansa alh ya susuce gaba 'daya ganin masoyiyarsa kwance rigis.

Mahaifiyar nyssa ita takarbi fannah tadawo hannunta kafin nyssa ta warke.

Shekara 'daya tana jinya allah yakarbi ranta wanda kuma gurin xuwa gaisuwar munafincine su haj bilki suka zomata da wani mugun aikin daya haddasa fitina gaba 'daya a familyn dan kuwa 'kiyayya mai zafi ta shiga tsakanin dangin nyssa dashi dan gani suke shine sanadi.
Hakama 'yar uwarsa haj nurat tayi mummunan fushi dashi tanajin wata irin tsanarsa shima haka yakejin duk tsanarsu dansun tsani matarsa haj zeenat.

Da haka ya tattara yabaro cairo yakoma paris gurin 'dansa dan yanda yakejin tsanarsu ko

fannah dake gurinsu bazai iya zuwa ya kar'ba ba.

Rayuwa tayiwa haj xeenat yanda takeso dan tuni tazama haj babba ga hutu da dukiya dasuka mufun ratsata.

Matsalar farko dasuka fara samu itace 'dansa tameer ya girma yazama saurayi yafara 'dorasa adukiyarsa sai abun yafara damunta sbd yanda ta tsani yaron dan ya'dau son duniya dana nyssa ya 'dora masa.

Tameer saurayine bamai wasu shekaruba dan duka duka shekarsa ashirin da biyar xuwa da bakwai,
Yarone 'dan gata fiye da tsammani,
Balarabene sak dan mum 'dinsa ya 'dauko akomai.
Dad 'dinsa baya boye sonsa agaban kowa.
Ganin 'kiyayya ta ginu tsakanin haj zeenat da tameer yasa ya tattarata yamaidota nigeria dan yanxu babu wani sauran sonta aransa kawai dai zaman ake hakama 'kiyayyar 'yan uwansa ta ragu aransa.

Barinta 'kasar yasa tameer yakoma cairo dan kula da kamfunan dad 'din nacan wanda wata sabuwar 'kauna da gata yatashi acan dan kuwa dan lelensu yazama wanda hakan ne yasa yake asangarce duk da ya girma amma idan ka gansa a waje ya iya ha'de gira ba wasa.

Zamansa a cairo yasa komai ya cahanxa masu rayuwarsu suke a nutse sai lokaci lokaci yakanje nigeria gurin dad 'dinsa duk da shima bai cika zama a nigeria 'dinba.

Wani zuwane dayayi meenah 'yar haj kareema tagansa tace ita duk duniya shi takeso
Shikuwa harya koma baimasan dazamantaba.

Awata dawowar ne suka aikata masa mummunan aikin tunanan yafara 'dan ciwon kai kafin ya tattara yakoma
Aiko yana komawa ciwo ya tabbata hauka.
Sannu ahankali abu yaki sauki
'Karshe dai dad 'dinsa yazo yadau 'dansa yafara yawon 'kasa 'kasa dashi amma an tabbatar masa da kwakwalwarsa ta juye.

Nijeria ya dawo ya damka kula da 'dansa ga dr sufyan wanda ya budewa babbar asibiti yana sakar masa dukiya.

Ahakane wani malami ya tabbatar musu da sammune.
Anyi neman maganin sammun har angaji ba wani sauki ga masu kula dashi sai guduwa suke sbd wahalar kula dashi shinefa karshe akayi masa aure dan asamu akula dashi dakyau kafin ya warke ya za'bi zama da matar ko rabuwa da ita.

TOFAH.....

🌕🌕👉mamuh geee
🌕⚜️DA'IMAN⚜🌕

Na

MAMUH GEEE

☆dedicated to☆
Husnah bbchoudiallo

86→90

TASHA......
kiran sallar asuba yasa ta'dan 'dago kanta tana kallon masallacin cikin tashar
Bata gani sosai sbd kumburin da idanuwanta sukayi dan tsabar kukan datake sharba har asuba 'din.

Maida kallonta inda tameer ke kwance tayi tana kallon yanda sanyi ke ka'da jikinsa yatakure yana fidda numfashi da sauri da sauri.

Duddubawa tayi taga inda ake diban ruwa taje ta 'debo tadawo tayi alwala ta tada tameer da 'kyar tayi masa alawa sukayi sallah.
Gari na'dan fara haske taga anfara gyar motoci zasu fara lodi ta mike tareda kamosa ta'dau jakar kayansu suka nufi motocin.
Da sauri wani yayo gurinsu yace ina zasu murya adashe tace kano.
Karbar kayansu yayi yasaka a mota suka shiga atsorace sai rabon idanu take sbd kallon da aketa binsu dashi dan ganinsu kamar larabawa ita buxuwa da zuriar hausawa shima larabe da xuriar hausawa.

Tameer gaba 'daya afirgice yake duk da baida lafiya

Ganin ana kallonsu saiya 'kankame nazli yana lafewa ajikinta
Mutane mezasuyi inba dariyaba ganin 'katon saurayi dashi yana boyewa bayan mace
Gashi a fuska kamar jarumi.

Dariya ake musu sosai harda tsokanarsu aka fara tana hawaye tayi saurin jansa suka fada motar suka xauna yana 'kankameta.

Hawaye take sosai har motar tacika suka tashi bayan ankarbi kudin motarsu.

Lafewa tameer yayi ajikinta yana kallon kyakkyawar fuskarta data kumbura
Ta'dan kallesa cikeda fargabar abunda zasu tarar atakai dakuma tsoron kada cimar can tayi masa mummunar illah akan wadda yake ciki.

Da rana tsaka suka isa kano ta fito rikeda hannunsa tashin hankalinta na tsananta ganin sun kusa isa kenan.

Motar 'kauyen takai suka shiga daga cikin tashar
Ga yunwa da 'kishirwa dake damunsu su duka hardai ita me juna biyu da duk kaganta kasan cikine da ita.

Karfe hudu suka isa takai ana saukesu ta rushe da kuka jikinta na mazari dan tun bata isaba takejin wani irin tsoro na shigarta musamman na cikin jikinta dabatasan yaza'ayiba.

Da 'kafa suka isa 'kofar gidan taja ta tsaya cak shikuwa tameer sai shige mata yake sbd tsoron yaran dake biyarsu tun a hanya suna cewa lah buxaye.

Hawayen idonta suka gangaro ahankali tasaka hannu na rawa ta shafesu tareda doka shahada tashiga tsakar gidan.

⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜

Zaune suke a tsakar gidan sunacin gyada suna rangada fira itada aminiyarta ta kullum wato iya jummai sai karima 'yar iya jummai dake 'dakin babah ladingo itada bubah suna firar soyayya cewar su babah ladingo amma kuma banda tumurmuxarta ba abunda yake a'dikin kuma sarai suna jiyosu amma sai firarsu suke cikin nishadi.

Ganin larabawa a gidan yasa suka mi'ke atare suna kallonsu
Babah ladingo tayi saurin juyawa zata 'dauko tabarma tana fadin,
Sannunku ba'ki kushigo.
'Ko'karin shinfida tabarma takeyi iya jummai data 'kurawa nazli dake hawaye ido tana mata kallon 'kurulla ta waro ido da 'karfi tace,

NAZLI

Kallon iya jummai tayi murya 'kasa 'kasa tace,
Jummai wace nazli kuma salon ki kore manasu 'kila ba'kin arzikine.

Da 'karfi taja bushashshen hannun ladingo takaita gabansu tana duba kigan......
Bata 'karasaba sbd cikin jikin nazlin data gani.

Tattakewa babah ladingo tayi ta zuba ihu tana kiran jamaa suzo su tayata ganin ankoro nazli da cikin shege datayo da aurenta.

A kidime su bubah suka fito yana gyara zaman wandonsa suma a firgice suke kallonta sai alokacin suka lurada balaraben dake bayanta nan take suka rufeta da duka har ita harshi

Ma'kabta suka taru ana kallo tareda yin tir da halin nazli datayo cikin shegen aka korota 'karshema cewa sukayi mai gadin gidanne buzu irinta yayi mata ciki aka korosu tare.

Labari yakai kunnen me gari ya aiko 'dan aike da wuri akan adaina dukansu akawo masasu yanxu yanason ganinsu dan bazasu zauna agarinsaba.

Koda sa'ko ya isa tuni dukkaninsu sun jima da suma tsabar duka.

Ruwa aka kelaya musu suka fara motsi
Ta bude idanuwanta dakyar tanajin wani irin ciwo tako ina ajikinta.
Cikin wata irin dauriya ta daddafa ta tashi zaune tareda jan jiki ta isa inda yake zube ko yatsa bai iya 'dagawa bakinsa da hancinsa na jini haka itama
Kuka tafashe dashi tana kiran sunansa agalabaice.

Ciccibarsa sukayi itama su iya jummai suka jata kawar kaya akayi fadar me gari dan ladingo ta gwammace ta kashesu data zauna dasu.

🌕🌕👉mamuh geee
🌕⚜️DA'IMAN⚜️🌕

Na

MAMUH GEEE

☆dedicated to☆
Husnah bbchoudiallo

91→95

Gaban me gari aka xubesu kamar kayan wanki ko motsi dakyar sukeyi anyi musu raunika bakyan gani.

Kallonsu yayi saiyaji wani tausayinsu yashigesa hardai na nazli dayasan mahaifinta sosai da mahaifiyarta kuma yana sane da ukubar datake ciki hartayi aure.

Gyara xama yayi yana kallonsu yace,
Dukan dakukayi musu bazai bari nayi wani hukunci ayanxuba dan haka abarta ta zauna gidan mahaifinta harta samu sauki sai adawo.

Yana fadar haka ya sallami kowa su babah ladingo kamar zata fashe tsabar ba'kin ciki tana fadin,
Ni yaushe wannen 'bakar zuri'ar zasu barni naji da'din rayuwata.

Da taimako suka iso gidan ladingo naxabgа musu harara kamar idonta zasu fado
Zuciyarta na tafarfasa kaman ta 'kone jitake kamar ya sha'kesu su mutu ta huta
Ta shige 'daki da 'karfi tana huci tareda mukarabanta.

Da bin bango ta isa kofar tsohon 'dakinta daya tsufa ya mutu duk ramukan cinnaku da 'beraye yacikashi sbd dama ba siminti ne dashiba.

Jiri na 'dibarta ta share 'dakin ta fidda zaninta 'daya ta shimfida a'kasa takoma takamosa ta kwantar dashi akai itama ta sulale 'kasa ko shimfida babu
Nan take suka fice hayyacinsu sbd zazzafan zazzabin dayayi musu mummunan kamu sbd azaba.

Ruwan randa me sanyin aka antaya musu bokiti guda

A firgice ta tashi zaune duk da ba 'karfi ajikinta ko kadan
Shikuwa idanu kawai ya iya budewa awahalce dan ko motsi baya iyayi sbd arayuwarsa baisan

wahalaba,
Jikinsa banda hutu da gyara ba abunda yasani shiyasa yake cikin azaba sosai.

Baba ladingo ce tsaye karima agefenta rikeda bokiti.

Cikeda ba'kin cikinta takalli shegen buzun ta 'karbi bokitin 'karfen hannun karima xata buga masa akai
Nazli tayi surin fadawa jikinsa bokitin yasameta a goshi tuni jini ya 'balle amma hakanan ta daure tana share hawaye.

Shewa ladingo tayi tana cewa lallai naga alamar akan wannnan ko'dadden zaki 'dau komai to muzuba nidake dan wallh su buba da iro da idi zansa su jibgarmun shege kekuma ni zanji dake.
Tashi nafasa korarku agidana aikin bauta zakuyimun koba komai nasamu bayi
Tashi maza wanki zakimun yanxu.

A ki'dime ta 'dago sbd tsakar darene gata tana cikin wani hali na ciwo da yunwa ina taga 'karfin wanki.

Kan tameer tayi da bokitin a fusace zata rafka masa cikin sauri ta mike tana cewa xanyi wankin.

Wata dariyar 'keta suka saki suna kallon wani sabon ikon allah.

Tana kallo yana rawar sanyi kamar zai shide sbd sanyi ake ga ruwan da aka zuba musu ga 'dakin ko 'kofa baida
Tana kallonsa ahaka ta fice tana hawayen ba'kin ciki.

Wankine kamar sunyi shekara basuyi dan harda kayan iya jummai danasu buba dana karimar dana ita ladingo hardana iro da idi.

Jikinta na rawa ta fara wankin ko gani batayi sosai ga hankalinta duk yanakan meer dake can kwance cikin ruwa da sanyi.

🌕🌕👉mamuh geee.
🌕⚜️DA'IMAN⚜️🌕

Na

MAMUH GEEE

☆dedicated to☆
Husnah bbchoudiallo

96→100

Wankine mai yawan gaske na dukkaninsu hardana iya jummai da 'danta iro,
Gana buba da idi hardana karima da ladingo.

A wahalce take wankin jikinta na mazari sbd zazzabin datake ciki ga sanyi dake kadawa sosai
Duk radadin datake ciki Gaba 'daya hankalinta nakan tameer data baro 'dakin kwance yana rawar sanyi cikin ruwa ga sanyi da ciwo.

Saida gari yayi haske sosai ta gama wankin dakyar ta mi'ke a duddu'ke tana tafiya dan bazata iya mikewaba.

'Dakin ta nufa tana hawaye dakuma  fargabar halinda zata samesa.

Kukane tareda farin ciki sukaxo mata lokaci 'daya sbd a zaune tasamesa jingine da bango yana bude idanu dakyar sbd azaba.

Da gudu ta fada jikinsa tareda sakin wani irin kuka mai ratsa zuciyar mai sauraro.

Saidata sha kukanta kafin ta mike tareda kamasa tana shirin canza masa kaya sbd ajike yake har alokacin.
Jakar kayansu ta duba bataga komaiba.
Ta sake dubawa da kyau ba kala ko 'daya aciki

Hayaniya tajiyo a tsakar gidan tana saurarawa saita jiyo rabon kayane suke
Da sauri ta fita tsakar gidan aiko kayansu kaf

Su idi,da bubah, da iro suka rabe kayan tameer
Nawa kuwa kaf karima aka ba.

Ahankali hawayenta suka cigaba da gangarowa ta juya takoma 'dakin tareda zama kusada shi ta cusa kanta a tsakiyar gwiwowinta tana rero kuka sbd.

Kiran tashin hankali ladingo tafara yo mata ta mike ahankali taje fuskarta duk ta kumbura sbd kuka.

Aikin gidan tasata harda 'diban ruwa tana gamawa taje tasiyo tameer koko
Tana basa yafara kelayo mata amai.
Hankali tashe take kallonsa harya gama
Ta goge masa jiki tareda gyare gurin.

⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜

Rayuwa ta zame musu u'kuba a 'kauyen
Tun suna jiran kiran me gari harta daina dan yayi watsi da zancen.

Ladingo kuwa duniya tadawo musu sabuwa dan tasamu bayi yanda takeso duk da itake duk aikin dazasu saka tameer 'din kasancewar yanxu agarin kowa yasan lalurarsa ta juyewar hankali.

Itake aikin gidan kaf
Tayi wankinsu kaf
Tayi 'dibar ruwa da abincin saidawar ladingo komai yawansa duk da aikin yafi 'karfinta.

Tun yana mata rakin cizon cinnaku harya daina yasaba

Yunwa kuwa tasamu kyakkyawan mazauni ajikinsu dan sunyi wata muguwar rama.
Fatarsu ta dafe ta lalace sbd sunma manta da wani sabulu ake wanka
Sunyi wani furi furi dasu.

Tameer yadaina ciwo sosai saidai haukarsa data fito muraran dan yanda idan zasu 'dibar ruwa suna tafiya yana tsince tsince
Hakama idan sukaje rafi cewa yake saiya fada ruwan yayi wanka
Ga yara da suke bibiyarsa suna masa wakar mahaukaci.
Abun nadamunta amma ba yanda ta iya.

Tun ana zaginsu da kyararsu har andaina anfara tausaya musu sbd ukubar dasuke ciki sosai.
Suturar sawama basuda ita dan kayansu sun ko'de harsun fara yayyagewa.

Ahaka Cikinta ya tsufa sosai kuma hakan take duk wahalar
Ta bushe bayan kashi ba komai.

Soyayyarta da kulawarta kullum akan tameer 'dinta suke,

shi kadai ke kawo murmushi afiskarta dan duk takallesa takanyi murmushi hardai idan tana aiki yana damunta da shirmensa.

⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜

Zaune take tana wanke wanke cikin sanyin jiki sbd tun daren jiya takejin ciwo ahankali amma take daurewa dan kota nuna ba me taimakonta.

Tana kallonsa yana wasa da ruwan wanke wanken amma takasa hanasa hartasamu ta gama dakyar.

Gyare gurin tayi ta'dau bokiti tana rintse idanu suka fice zuwa 'dibar ruwa.

Shike rikeda bokitin itakuma tana tafiya ahankali sbd ciwonta yafara tsananta.

Wata mata data shigo 'kauyen rikeda 'yar ledarta harta giftasu saita 'dan dawo tana kallon nazli tace,

Yarinya gidan malam adamu headmaster nake nema dan ya'dan 'bacemun.

Lumshe idanu tayi ta budesu dakyar cikin 'dan kannewa tace,
Ya rasu tunda dadewa.

Salati matar tasaki cikin rawar murya tace,
'Yarsa fa tanan?
Dan allah nunamun gidan.

Cikin ciwonta daya fara fin karfinta tace,
Ni..ni nice 'yarsa.

'Kara dam'ke hannun tameer tayi duk da tana cikin ciwo dan zai iyayi wani gurin.

Akidime ta 'kurawa fuskar nazli ido
Sai alokacin matar ta lura da halinda nazli take ciki

🌕🌕👉mamuh geee
🌕⚜DA'IMAN⚜🌕

Na

MAMUH GEEE

☆dedicated to☆
Husnah bbchoudiallo

101→105

Kamota tayi tana kiran sunanta dan 'kokarin durkushewa take kuma har lkcin takasa sakin hannunsa

Matar takalli tameer dakeson kwace hannunsa ya hango kara yanason yaje ya 'dauko.
Kamata tace masa tana kamo nazli 'din
Kallonta yayi yana son boyewa bayan nazli.
Cikin azaba tace bashida lafiyar hnkli.

Kamata tayi suka koma gidan dakyar
Kai tsaye 'dakinsu suka shiga zuwa lkcn ciwo take sosai.

Bakowa agidan dan basanan sunje wani 'kauye bikin suna.
Kwantar da ita matar tayi dan dama itake karbar haihuwa garinsu.

Cikin ikon allah babu 'bata lokaci ta haihu lafiya 'kalau.

Ruwa matar ta 'dora tayiwa yaron data kirada balarabe sbd tsantsar kyawunsa data gani wanka.
Kama nazli tayi tayi mata wanka tas kuma allah yasa bayau su ladingo zasu dawoba.

Nade yaron sukayi axanin bakuwar dan babu kayan daza'a saka masa.

Ido ta 'kurawa yaron tana hawaye dan tasan bazai samu rayuwar jin da'di kamar yanda taso masaba.

Kuka take rerowa harda shesheka matar nakallonta harta gama ta matso kusada ita tace,
Sunana INNAH ASMAH
Tareda mahaifiyarki nataso akayi mana aure tare
Tun rasuwar baffana data mahaifiyarki ban 'kara xuwa garinnanba sai yanxu naxo sbd na duba

'yar rahane ashe har malam yarasu an miki aure.

Hakanan ta kwashe komai kaf tafada mata tana kuka sosai.

Ita kanta innah asmah hawaye take tana sharce majina kafin ta mike tana cewa
Nazli wahalarki insha allah takare dan bazan barkiba dake xan tafi.

Mikewa tayi tafice afusace tana sharce hawaye.

Sai alokacin tameer yashigo 'dakin kayansa sharkaf da ruwa dan tunda suka shigo yanacan tsakar gidan yana 'bata ruwan ladingo allah ma yasa basanan.

Da sauri yazo kusa da ita yazauna yana kallon 'dan jaririn dake hannunta yana keta kuka ta rasa yazatayi sai kukan take itama.

Washe hakora yayi yana 'kokarin tabashi saiga innah asmah tayi saurin karbar yaron tareda saka masa kayan dataje tasiyo yanxu.

Duk wani abun bukata tayi musu dan kwananta biyu kafin su ladingo suka dawo sunyi mamakin ganin na haihu amma ganin innah asmah yasa sukayi biris damu dan tace sai bayan sati zata koma.

Tameer kuwa wawa yakoma kan yaron dan rigima yakeyi sosai sai anbashi jaririn
Tun innah asmah najin tsoro harta daina dan sosai yake nuna son yaron.

Sati nayi suka radawa yaron suna ZAID
Nazli nakiransa da WALEED

Sun 'dan walwale cikin 'yan kwanakin sbd samun cima mai 'dan kyawu da kula da innah asmah ke musu.

Kwananta goma cif ta ha'da kayanta zata tafi da niyyar zata dawo ta tafi dasu wani satin.

Hawaye nazli keyi sosai bayan tafiyar innah dan tasan zasu komama wahalane
Amma idan ta tuna daxata dawo ta tafi dasu saitaji wani sanyi aranta.

⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜

Ahankali dai sai gasu sunkomawa wahalarsu ladingo ga nauyi daya 'karar mata na waleed allah

ma yasa tameer takebawashi su zauna 'daki tayita aikinta.

Tun tana lissafin dawowar innah harta daina sbd fiyeda wata uku kenan amma babu ita.

Wahalarsu ta yanzu hartafi tada dan tuni suka 'karmaje dukkansu hardai ita dake shayarwa.
Kullum dare kwana take kuka,
Ko aiki take hawaye takeyi sbd tausayin rayuwarsu.

Kamannin waleed sun fito sosai da tameer dan kuwa kamar tasu hartayi yawa.
Ga wata irin shakuwa dake tsakaninsu danko ita wani xubin yafison tameer da ita.

Muguntar dasu bubah kewa waleed yasa bata bari suna fitowa tsakar gidan kullum suna 'kunshe adaki.

Akwai ranar da waleed yayiwa ladingo 'barin gari aiko buba yayi ball dashi
Ladingo kuwa ruwan talginta ta zuba masa ahannuwa harda sumewa yayi
Ranar basuyi bacciba kwana sukayi zaune suka kuka harda tameer 'din sbd yanda yaron hannuwansa suka sale ga wani irin kuka dayake sbd zazzabi da azaba.

Komai ya ida jagule musu wuya tayi wuya
Ga waleed yagirma sosai harya iya magana
Sunkoma suturama saida fadar mai gari taji tausayinsu aka basu kala biyu biyu wanda daga gani kayan sun jima da mutuwa amma haka suka karba suna sawa.

Babbar damuwarta baifi waleed da bayajiba gasu sukuma sukamasa suyi masa dukan tsiya kamar wani 'kato 'dan uwansu.

⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜

Zaune take tana bawa tameer ruwa sbd ciwo dayake fama dashi tun daren jiya.
Waleed ya shigo 'dakin da gudu yana haki yace,
Anty kinga wata tana nemanki gatanan xuwa.
Zaunar dashi tayi tana cewa,
Waleed bana hanaka yawoba.
Allah anty banje yawoba ina 'kofar gidafa.

Sallamar innah asmah ya hanata yin magana ta mike da gudu ta rungumeta tareda fashewa da kuka.

🌕🌕👉mamuh geee
🌕⚜️DA'IMAN⚜🌕

Na

MAMUH GEEE

☆dedicated to☆
Husnah bbchoudiallo

111→115

Wani wawan haushin kare yaji daga nesa baisan sanda ya juyo da gudu ya fa'da gonar wani wawan jiri da sarawar kai ya ziyarcesa amma baitsayaba saidaya kai tsakiyar titin wanda yayi daidai dakawowar wata mota aguje tayi sama dashi ya zube cikin jin.

Akidime nacikin motar yafito yayo kansa yana salati sbd ganinsa cikin jini
Juyosa yayi da sauri dan 'daukarsa yakaisa asibiti tunda shi likitane abun zaixo da sauki insha allah.

Zabura yayi da 'karfi ya ware murya yace
TAMEER

Jikinsa har rawa yake yadaukesa yasa amotar ya figeta da wani irin speed sai kano.
Asibiti ya wuce dashi kai tsaye aka shige dashi emrgency.

Waya dr ibraheem ahmad ya fiddo wayarsa jiki na rawa ya lalubo wata number ya danna kira.

⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜

ABUJA

Zaune yake cikin tangamemen palonsa
Idanunsa sanyeda farin medicated glass

Yayi xurfi cikin tunani da damuwa

Yau tsawon wata shida kenan da allah yabasa sa'ar kubutowa daga 'yan ta'addan dasuka sacesa suka rufe
Tunda yadawo yasamu bayanin  'bacewar 'dansa da nazli abakin matarsa datayita kukan munafuncin cewar ba'asan inda sukayiba anyi nema har angaji.

Wannan mugun labarin saidaya haddasa masa kwanciya asibiti tsawon wata biyu a newyork kafin yadawo aka baza bincike tako ina.

Wayarsace tayi ringin harta katse bai dubi inda takeba.

Haj xeenat data shigo palon cikin ado tana she'ka 'kamshi takalli wayar dan ansake kira tamaida kallonta garesa tana zama kusa dashi tareda 'daukar wayar sbd sunan dr ibrhm data gani dan sam tana kasa nutsuwa a duk lkcn dataji yakira alh zaid sbd tsoron yafada masa komai gameda abunda yafaru.

Arikece yake fadin,
Alh...alh tameer....gashi nnan asibiti

Wat ta fa'da da 'karfi tana mikewa cikin wani irin tashin hankali
Jikinta nan take ya'dau rawa.

Alh zaid kuwa wayar ya warta da 'karfi yana sauraron bayanin dr ibrhm aibai tsaya jin sauranba yafice palon baikobi takan haj xeenat dake daskare agurin tana aman xufa.

Motoci uku na alh zaid da securites suka 'dau hanyar airport adaren dan xuwa kano.

Wuraren asuba suka sauka kano kai tsaye asibitin suka wuce
Alh zaid naganin yanda tilon 'dansa yakoma ya yanke jiki yafadi.

Yana farfadowa ba'a tsaya komaiba ya ha'da 'dansa da dr ibrhm suka bar 'kasar zuwa germany.

********

Jinyarsa ake ana kula dashi sosai a garmany 'din dan tuni su haj nurat suka isa germany 'din suma.

Watansa 'daya akwance kuma anasa ran farfa'dowarsa ko wane lokaci.

Haj nurat ce da fannah zaune a'dakin.

Haj nurat waya takeda ammah mahaifiyar nyssa tana fada mata yanayin jikin nasa
Fannah kuwa chattin takeyi da tsadaddiyar wayarta.

Ahankali yafara bu'de idanunwansa dasukayi masa nauyi sosai yana gani dishi dishi harsuka bu'de.

UMMEE ya fa'da muryarsa bata fita amma cikin sa'a kuwa haj nurat taji hakama fannah.

Rige rigen isa gurinsa suke cikin tsananin farin ciki wanda yayi daidai dashigowar alh zaid

Farin cikin dasuke ciki baya misaltuwa dan kuwa tameer ya warke ras yadawo cikin cikakken hankalinsa kamar kowa.

An sanar da 'yan cairo dabasu sabu xuwa kowa murna yakeyi anata farin cikin.

HMMMMMNN  WATA SABUWA KENAN.

🌕🌕👉mamuh geee
🌕⚜️DA'IMAN⚜🌕

Na

MAMUH GEEE

☆dedicated to☆
Husnah bbchoudiallo

106→110

Zaunawa sukayi tana lallashinta tace,
Nazli kiyi hkr rashin lafiya nayi sosai kuma maigidana ya rasu shiyasa ban dawoba amma yanxu gani nazo kuma ayau zamu wuce basai gobeba.

Sharce hawaye tayi gabanta na faduwa hakanan taji gabanta yafa'di da tafiyar.

Kallon tameer tayi kafin tamaida kallonta ga inna tace,
Inna meer bashida lafiya yazamu iya tafiya dashi.

Kadaki damu tunda zai iya tafiya muje damun shiga mota zai aishikenan.

Ha'da 'yan tsummansu tayi tana share hawaye dan sam ta rasa nutsuwa batasan dalili ba.

Kamo tameer tayi inna ta riko hannun waleed dake murnar zasuje yawo.
A tsakar gida suka samu ladingo da iya jummai suna she'ka firarsu
Suna ganinmu suka 'daure fuska suna harare harare.
Inna ce tayi musu bayanin xata tafi damu har xuwa samun saukin tameer.

Harara iya jummai ta watsowa inna tana fadin,
Dan wa'innan dangin buxayen masu kama da figaggun kaji to tafi dasu ko aminiyata da 'yayanta sa huta da ba'kin iri.
Ladingo kuwa ko kallo basu isheta ba sai ka'da kafarta take.

Ficewa sukayi jiki asanyaye.
Dakyar suka samu motar 'kauyensu inna.
Tunda suka baro gida takasa tsaida hawayenta tana tunanin yaushene zata samu kyakkyawar rayuwa?
Itakenan kullum garari yanxuma batasan wace rayuwa zasuyi acanba.

Da maraice suka isa 'kauyen da 'kafa suka isa gidan inna.
'Dan 'karamin gidan 'kasane mai tsakar gida da 'dakuna biyu sai 'dan 'karamin ban'daki atsakar gidan.

'Daki 'daya tabasu suka share tsaf tabasu tabarma suka shimfida tareda aje 'yan kayansu.

Sanwar abinci inna ta 'dora musu tana gamawa tabasu sukaci suka 'koshi nan waleed yafara wasarsa itakuwa share gidan tayi tas
Ana kiran sallah sukayi sallarsu har lkcn kwanciya yayi suka kwanta.
Washe garima da kanta ta gyare gidan tayi duk aikin gidan inna na yaba mata sosai sbd tayi 'kokari.

Chanjin rayuwa yazo musu sosai sbd yanxu harsuna dariya su 'kyakyata
Ga yunwa tuni ta gudu ajikinsu
Sunyi 'danyi kyawun gani dan yanzuma kamannin tameer da waleed ke 'kara fita abun har tsoro

yake bata
Ga muguwar sha'kuwar dake tsakaninsu sbd waleed yasan tameer shine babansa.
Hankalinsu yanxu akwance yake basuda matsala sbd inna asmah nada rufin asiri sosai sbd tanada dabbobi da yawa ga sanaar saida kayan 'kulle 'kulle datakeyi.

⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜

4 month later

Tun jiya takejin jikinta asanyaye da faduwar gaba har saida inna ta tambayeta lafiyarta 'kalau kuwa
Tace lafiyarta 'kalau.

Zaune suke tsakar gidan inna na 'daura kuka datake saidawa nikuma ina wanke wanke.

Waleed da tameer ke wasarsu suna dariya sai waleed ya 'dale bayan tameer ya goyasa yazagaya tsakar gidan dashi ya saukesa saiya juya waleed yana 'kokarin shima wai waleed 'din ya goyasa.

Daria muka saki duk mu duka waleed ya gudo bayan inna yana cewa,
Inna dubi wai saina goyasa babba dashi fa.

Daria inna tayi tana cewa,
Aini bana shiga tsakaninka da babanka nazo naji kunya anjima dan nasan shiryawa zakuyi.

Da gudu waleed yabar bayan inna yana daria shima tameer dariyar yake
Nazli ta 'kura masa ido sbd kyawun dataga yayi mata sosai wanda rabon datayi masa irin kallon harta manta
Wani sabon sonsa takeji yana sake tsima azuciyarta.

Waje sukayi dukkansu suna daria itakuwa taci gaba da aikinta inna ma hankali ta mayar anata aikin.

'Boyewa waleed yayi bayan bishiyar 'kofar gidan tameer yawucesa batareda yagansa ba
Shikuwa yana ganin ya wuce fito ya zauna 'kafar gida yana wasar 'kasarsa.

Tafiya yaketa famanyi shi ala dole saiya kamo waleed haryayi nisa sosai.

'Karyen 'kauyen yakai ammai bai tsayaba sai kawai yaci gaba da tafiya tun yana gani har duhun mangariba yasawo kai nan take tsoro yafara kamasa
Yafara waiwaye yana tafiya da sauri sauri.

Har duhu yayi sosai gudu yake ketawa adajin kamar ba mutumba.

Daidai wata gona yakai ya tsaya cak kamar an tsaidashi.

Gonar wani bawan allah ce dayayiwa wani kyakkyawan asiri sbd 'barayi duk wanda yashiga gonar indai yanada asiri ajikinsa to zai karye ko wane irine.

Soyake ya keta gonar ya wuce yakasa dan tsananin tsoro sbd titin daya hanga motoci na wucewa da mugun gudu dazarar ka wuce gonar.

Juyawa yayi da sauri dan komawa inda yafito.

🌕🌕👉mamuh geee
🌕⚜️DA'IMAN⚜🌕

Na

MAMUH GEEE

☆dedicated to☆
Husnah bbchoudiallo

116→120

Gab da magrib ta le'ka 'kofar gidan taga waleed ka'dai tace,
Waleed kudawo gida lkcn sallah yayi
Ina meer 'din yake?

Kwaso kayansa wasansa yayi yana cewa,
Tun tuni fa yatafiyarsa yawo nika'dai nake wasana.

Dam. Gabanta ya buga  tareda ha'de wani yawu da'kyar tafito wajen gaba 'daya ko hijab babu ta riko waleed ta jijjigasa da 'karfi tace,

Waleed ina yatafi?
Kuma tun yaushe?

Anty tunda muka fito baiko tsayaba fa yawuce yabi can.
Yayi mata nuni da hanyarda tameer 'din yabi.

Cikin gidan takoma a ki'dime jikinta na zuba wani irin 'bari tajawo hijab tasaka a birkice tana 'kokarin ficewa inna tayi saurin kiranta tana cewa,
Lafiyarki kuwa inata tambayarki kina 'kokarin ficewa hijab ajuye?

Hawaye suka tsinke mata cikin rudewa tace,
Inna meer bayanan wai wai baya 'kofar gida ya..ya..y  sai kawai ta juya ta fice da sauri
Hijab inna tasaka tabi bayanta da sauri sukabi inda waleed yake nuna musu yabi.

Yawon nemansa suka fara suna tambayar duk wanda suka hadu dashi har akayi magrib babu wata alamar ganinsa.

Kuka take wanda ya gagara tsayawa jikinta
Sai mazari yake saida inna ta ri'keta sbd ganin yanda take neman xubewa dan gaba 'daya a ki'dime take
Waleed ma dayaga halinda antyn tasa take ciki saiya fara kuka.

Har 'karfe goman dare suna yawo saida suka zagaye 'kauyen tas amma babu alamarsa.

Da'kyar inna takamota dajan 'kafa suka dawo gidan suna shiga ta sulale 'kasa tareda sakin kuka da 'karfi tana kiran sunansa.

Kuka sosai take tana kiran sunansa cikin wani irin ra'da'di da ciwo a xuciya,

Yanda take kukan ne kamar ranta xai fita cikin wani irin hali yasa hawaye tsinkewa inna na tausayinta dakuma tunanin wane hali tameer 'din yake.

Kamata inna tayi tana 'kokarin tadata sai kawai taga ta zube idanuwanta arufe.

Salati tasaki tana yayyafa mata ruwa cikin ru'dewa dan yanda take ganin wani irin tashin hankali daga nazli 'din dan tasan tameer ya 'bata amma tasan nazli zata shiga mummunan halinda yafi wanda zaije yashiga sbd ganin idonta taga yanda naxli ke masifar sonsa fiyeda komai.

Tana farfadowa tasaki siririn kuka ahankali inna takaita 'daki tana bata 'karin gwiwar zaa gansa

insha allah.

A daren ranar basuyi bacciba sbd halinda nazli tashiga dan kuka take babu alamar tsayawa har shi'dewa take
Inna hankalinta ya tashi sosai dan tsoron kada wani abun yasamu nazli acikin wannan halin ga waleed ma saidaya sha kukan akaisa gurin tameer kafin inna ta lallabasa da'kyar yayi bacci wanda hakan ya 'kara 'daga hankalin nazli.

*********
Duk iya yanda inna ta tsammaci abun ya wuce nan dan saida 'yarta tilo guda sa'adah dake aure a kano tazo dan taimakawa halinda ake ciki
Dan ciwo rigis nazli ta kwanta bayan sun share kusan sati biyu kullum suna yawon nemansa har 'kauyukan kusa dasu sunje amma ba wani alamarsa.

Tayi wata muguwar rama,kuka da tunaninsa sun zama abincinta,
Inna tayi iya yinta amma babu wani sauki har ciwo yayi mata mugun kamu.

Inna da sa'adah sosai suke kula da ita har saida tayi wasu sati biyun akwance kafin taji sauki amma ba'a zuciyaba dan kuwa batajin zata ta'ba iya cire tunaninsa aranta.

Duk lokacin data tuna cewar bashida kowa ayanxu sai ita gashi tayi sakaci tabari ya 'bata.
Al'kawarin datayi na kula dashi yatafi abanxa yakasa kula da tameer 'dinta,
Tameer 'dinta datakejin rayuwa babusa batada amfani agareta.

Duk wani so da 'kauna ta tattara ta 'dorawa waleed,
Shikansa waleed kullum saiya musu rigimar abbansa saisun lallabasa.

Ahaka har wata biyu suka shu'de musu kuma tana 'dan sakewa wani lokacin amma shikam kuka kullum daren allah saita sha'ki abinta.

🌕🌕👉mamuh geee
🌕⚜️DA'IMAN⚜🌕

Na

MAMUH GEEE

☆dedicated to☆
Husnah bbchoudiallo

121→125

TAMEER☆

Yaji sauki sosai ya warware kamar bashiba
Kowa ji yake dashi kamarsu ha'desa.

Cairo yayi zamansa dad kuwa suka koma tareda haj xeenat datazo dubasa itama.

Dad dakansa yasa ayi masa binciken inda nazli take bayan yadawo sbd tameer sam baisan komai gameda ciwonsaba hasalima sun 'boye masa hauka yayi sun fada masa cewar kawai yasamu accident ne.

Duk iya yadda dad yaso asamo masa inda nazli take ba'a samu ba haka ya hkr yana adduar allah ya bayyanota kodan auren 'dansa dake kanta.

Watansa biyu a cairo yakoma asalin balarabensa yayi wani irin jajir dashi,
Yakoma asalin tameer 'dinsa 'dan gaye da tsafta ga class ga nera tuni 'yar tsohuwa ammah(kakarsa mmn nyssa)tafara masa maganar ita aure takeso yayi.

Hutawa yakesonyi sosai kafin ya koma office dan haka ya shirya ya wuce 'kasar america.

⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜
5month ltr

Watansa biyar cif a america yana cikin kwanciyar hankali da hutu
Ya xabga wani irin kyawu na ha'kika,
Fatarsa ta 'kara kyawu na musamman sai she'ki take alamar hutu ya ratsata sosai.
Duk wanda yagansa zai 'dauka mawa'kin nanne na larabawa me suna tameer housny.
Wani kwarjini da annuri ke fita afuskarsa da duk wadda takallesa saita 'kara kallonsa komai haduwarta da ajinta.

Jirgin cairo yabi yana sauka motocin kamfaninsu nanan akaxo 'daukarsa.

Sanye yake cikin black jins da red shirt data maseefar yimasa kyawu,sai wasu ha'daddun takarma ba'kake da agogon diamond rolex dake 'daure ahannunsa.
Fuskarnan sanye da gogls baki sai hakan yasa kyawun jajayen lips 'dinsa suka 'kara fitowa ga gashinsa dayasha gyara sai she'ki yake.
Wani irin 'kamshi ke tashi ajikinsa na turaren signature designer na maza.

Kai tsaye gida aka nufa dashi saidaya huta yayi wanka kafin yashirya ya tafi gidan umminsa wato haj nurat.

Tana ganinsa farin ciki ya bayyana afuskarta yazo ya rungumeta yana cewa,
I miss you so much my ummi.

I miss you too tameer ta fada tana jan kumatunsa.

Fannah ce ta fito 'daki rikeda waya tana magana da daddynsu aitana ganinsa ta katse kiran tareda fadawa jikinsa tana nurnar ganinsa.

Rungumeta yayi shima yana murmushi ya 'dago fuskarta yaja dogon hancinta irin nasa yana cewa,
My fannah has grown up but still acting like a bby.

Turo baki tayi tana cewa,
Pls B. Tafada cikin shagwaba.

Ammi kallonsu take cikin tsananin 'kauna tana 'karajin sonsu aranta.

Nandanan aka gyare dining cikeda abinci kala kala sbd shi kawai.

Sam bai wani ci abincinba dan bayason abinci da yawa.

Yana gamawa shida fannah suka fita zuwa gurinsu ammah.

Dakansa yake tukin cikin nishadi sbd ganun 'yar little 'kanwarsa dayakeso fiyeda komai tana taredashi.

A gidansu ammah suka kwana dan yanda tsohuwar ta rikice masa akan lallai aurensa takeson gani
Dakyar ya lalla'bata hardai saida suka kwana agidan.

Satinsa 'daya a cairo ya shirya yadawo nigeria dan sam ji yake kamar komai nasa farin cikinsa,ruhinsa,rayuwarsa duk jiyake kamar suna can.
Tareda fannah suka taho dan hakanan yanxu bayajin zai iya rabuwa da 'yar 'kanwarshi bare yanxu dazai zauna nigeria gaba 'daya.

Dad da kansa yazo 'daukarsu tareda direbansa
Yana ganin 'yayan nasa ya rungumesu cikin farin ciki da tsananin 'kaunarsu.

Kai tsaye sabon 'katon gidansa mai kamada mention dake asokoro.

Babban gidane mai 'daukeda sashe biyu
'Daya na dad da haj xeenat sai 'dayan na sir tameer.

GODIA ME TARIN YAWA DA RASHIN IYAKA GAREKU MASOYAN DA'IMAN🙏😘😘😘😍😍😍😍😍

🌕🌕👉mamuh geee
🌕⚜️DA'IMAN⚜🌕

Na

MAMUH GEEE

☆dedicated to☆
Husnah bbchoudiallo

126→130

Haj xeenat nacikin tashin hankali sosai sbd dawowar tameer harda 'karin 'kanwarsa fannah

wadda ta gani 'baro 'baro daga dad 'din har tameer ji suke da ita kamarsu ha'diyeta.

Babban tashin hankalinta baifi boka dayace aiki bazai 'kara kama 'daya daga cikinsu
Sannan gasu liloh sun gudu sunbar 'kasar sbd alh zaid yasansu su suka kamasa dan haka itadasu haj bilki sun basu kudi masu yawa sunbar nan sbd kada akamasu su fa'di sunayensu amatsayin wa'inda ke sasu aiki.

Yanxu batada wata sauran dabara data wuce tayi amfani da kissa tasamu yanda takeso dan ta tabbatar da baxata hutaba saitaga bayan tsinannun dangin larabawan.

Gate biyune da gidan
Na farko securitys ne xube agurin kuma anan duk wasu masu aiki ke tsayawa.
Saina biyu idanka shege na farkon shikuma motar masu gidanne kawai keshiga dan duk ba'ki da sauran motacin tsaronsu duk a harabar gate 'din farko ake barinsu.

Harabar gate na biyu kuwa duk motocinsune na musamman jere agurin parkin space.

Fa'dar tsaruwar gidan tabbas zaicinye page 'din gaba 'daya amma ku kwatanta irin yadda gurin zai tsaru.

Flowers ne masu kyau da tsada a harabar gurin ga fitilu masu ban sha'awa rufi da pentin gidan kawai abin kallone.

Babbar 'kofar palon shiga palon gidance agurin sai 'kofar garden 'din gidan.

Steps uku zaka taka kashiga ha'daddiyar babbar 'kofar palon.
Palon ya hadu ya tsaru sosai da royal kushins brown sai komai na palon shima brown tun daga kan cuttons 'din da center crpt,dasu manyan frames daduk wani abun dake palon dan hatta splite a.c guda biyarne a palon.

Opposite da dining area dake palon matattakar benene guda biyu suna kallon juna
'daya na hayewa palon tameer da two bedroms dinsa aciki,
Sai 'dayan na hayewa 'bangarensu dad suma amma nasu palo da tree bedroms.
Palon 'kasa 'din akwai wani palo ha'dadden palo da bedroom 'dinsa aciki wanda aka gyaresa tsaf da komai mai kyau da tsada sbd fannah.

Kwanansu biyu da dawowa tameer yafara fita office
Hakama haj xeenat ta maida hankali sosai gurin nuna musu so da kulawa na munafinci wanda ba 'bata lokaci ta siye xuciyar fannah tuni dan wani gata da ririta take nunawa fannah
Itakuwa fannah dama 'yar tagace sai kawai rasaki jiki tana shagwabarta son ranta

Kafin kace me tameer sbd son dayakewa fannarsa saiya fara girmama haj xeenat sosai hardai idan ana dining cin abinci ta kulawa kamar tabasu abaki.
Hankalinsu ya kwanta sosai sai rayuwar jin dadi suke da mum kaman yanda suke kiran hj xeent.

**********
Cikin nutsuwa yake saukowa daga stairs 'din yana sanye cikin black suit sai 'kamshi yake ya xuba kyawu iya kyau.
Fannah tayi saurin mikewa ta tarosa tana cewa,
Gud morning b.

Morning my little,

Daria tayi tana ce masa,
B pls inason xanbi mum biki xuwa kano
Pls kabarni nabita.

Xama yayi kan dining table 'din yana gaida dad da haj xeenat
Kafin cikin isa da class 'dinsa yace,
Little ure not goin anywhr for now but kibari next mnth am goin there for some work sainaje dake.

Shagwa'be fuska tayi tana kallonsa kamar xatayi kuka tace pls b.

Haj xeenat tasaki murmushi tace,
Alh kasa baki b yabarta taje mana.

Aa kunfi kusa amma bari nataimaka muku.
Kallon tameer dake kur6an black tea yana duba jaridar yau yayi yace,
Son kabarta sutafi since bata ta6a zuwa kanon ba dama and its just a matter of 5 days.

Kallon agogon diamond 'din dake hannunsa yayi yace,
Shikenan dad since ka amince da tafiyar
Mikewa yayi tareda kwasar wayoyinsa yafice dan yanada meeting 9 gashi har 9 'din tayi.

B what tym xaka dawo yau sbd i wnt to spend sumtimes wit you cox all diz days bakada tym 'dina koyaushe busy.

Kafin yabata amsa MEENAH tashigo harabar gurin cikin wani irin ado najan hankali tana sanyeda doguwar rigar pink lace ya kamata tasaka wasu heels masu shegen kyau sai 'kamshi ke tashi ajikinta.

Tun kafin ta iso gurinsu zuciyarta ta buga da 'karfi
Tunda allah ya halicceta bata ta'ba ganin ha'dadde,kyakkyawa,cikakke mai class kamarsaba.
Wani gigitaccen sonsane ya daki xuciyarta nantake tayanke tasamu mijin aure.

Shafo fuskar fannah yayi yace,
Take care lttle
Yafada motar direba yaja suka bar gidan.

Kallon fannah meenah tayi tareda sakin murmushi dan sai yanzu tagano sune 'yayan mijin mummy xeenat 'kawar mummynta.

Gaisawa sukayi fuska asake kafin suka shiga palon daidai nan dad yafito shima yabar gidan.
Rungumesu haj xeenat tayi tana farin cikin ganin meenah kafin suka 'dunguma xuwa cikin palon.

🌕🌕👉mamuh geee
🌕⚜️DA'IMAN⚜🌕

Na

MAMUH GEEE

☆dedicated to☆
Husnah bbchoudiallo

131→135

Agidan ranar meenah ta yini tanata faman jan fannah ajikinta harsaida suka saba sosai
Ta girmi fannah da kusan shekera hudu amma haka dan tanada 24 fannah kuma nada 19.
Kamar kadasu rabu haka meenah ta tafi da motarta
Tana isa gida ta fada jikin mummynta cikin farin ciki tace,
Mummy nasamu wanda nakeso zan aura tameer 'din gidan mummy xeenat.

Wani farin ciki haj karima taji dan dama tundata 'kyalla ido akan tameer taga yanda dukiya da hutu tareda jin dadi suka kwanta masa taji tanason meenarta ta auresa dan zasu samu dukiyarda suke burin samu tuni.
Kallon 'yarta tayi tana cewa,
Bby ai kuwa kinyi miji dan idan har ni haj karima ina yawo saikin auri tameer kin haifamun larabawan jikoki.
Cikin farin ciki ta rungume mummyn tana fadin i love you mum.

Ta waya haj karima takira haj xeenat tayi mata bayanin komai haj xeenat harta kusan fin haj karima farin cikin hakan nan suka hure kunnan meenah suka koya mata kissoshin dazatabi ta mallakesa wadda ta farko itace ta siye zuciyar fannah wadda ita xata saka tameer yaso meenah tunda yana maseefar son 'kanwar tasa zai iya komai akanta.

************
Burin meenah yacika dan kuwa yanxu sun 'dinke da fannah sun zama aminan juna
Kullum suna gurin yawon shopping ko gurin shakatawa
Tameer kuwa ya maida hankali sosai akan aikinsa sai kudi dayake sakar musu dan tun yana 'daurewa meenah fuska harya 'dan fara sake mata ka'dan sbd shakuwarta da little 'dinsa.

⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜

'Karfe biyar jirginsu yasauka a airport 'din kano sbd bikin dasuka xo na 'yar 'kawarsu mummy.
Fannah,meenah,mummy karima da mummy balki ne kawai sukaxo mummy xeenat bata samu zuwaba sbd wani uzuri.

Daga airport gidan haj karima dake kanon suka dosa
Babban gida mai kyau dashi ba kowa sai mai gadi da matarsa dake kula da gidan.

Sa'adah 'yar inna asmah itace matar me gadin gidan kuma 'yar aikin haj karima ita ta gyare gidan tsaf tana musu barka da xuwa suka amsa fuska asake kafin kowa ya wuce daki dan hutawa ita kuma ta shiga kicin tafara ha'da musu lafiyayyen abinci.

'Kamshine yacika ko ina agidan na girkin datake tana gamawa ta jere a dining nan duk suka fito kowa yayo wanka yafito cikin shigar shan iska dan sai jibine ma xa'a fara bikin.

Saida kowa yazauna dining kafin fannah ta fito daga bedroom cikin 3 quater jins pink da farar vest ta 'daure gashinta dakw lilo har kan bayanta tana waya da b 'dinta.

Saura 'kiris sa'adah tasaki drinks 'din data dauko a tray zata kai dining 'din sbd ganin fannah. Ido takura mata tana ha'diye wasu yawu dakyar sbd fuskar waleed 'din nazli 'dinsu data gani sak a fuskar fannah hatta 'dan dimple 'dinsa da dariyarsu komaima sak gashinan illah hutun dake fatarsu ya banbanta.

Dakyar ta iya kai tray 'din ta aje tana yiwa fannah data gama wayar ta zauna barka da fitowa
Cikeda fara'a ta amsa tana cewa,
Lallai xanji 'dadin abincin nan dan 'kamshinsa na da'di.

Daria kowa yayi banda sa'adah data 'kara gigicewa sbd maganar da fannah tayi ya 'kara fiddo da tsantsan kamanninta da waleed.

Suna gamawa ta tattara gurin takoma tana cigaba da aikinta.

Kano tayi musu da'di dan kuwa shakatawarsu suke kafin afara biki sbd kullum suna yawon gari dan yanxu ba 'karamar dukiya suke samu ta gurin fannah ba dan kudi sosai tameer ke sakar mata.

A 'bangare 'daya kuwa wata irin shakuwa tashiga tsakanin sa'adah da fannah dan sosai takeson aikin sa'adah sbd tsananin tsaftarta da iya girkinta ga barkwanci da saurin sabo. Jitakeyi badan sa'dah nada aureba da da ita xata tafi dan tanada bukatar 'yar aikin kanta acan sbd duka duka nafeesat ce kawai me aikin mummy dan haka tana bukatar me kula da tsaftar gurin b 'dinta dakuma nata gurin.

Fira sa'adah take mata tana yanka mata fruit sukadai ne agidan dan su mummy sun fita meenah kuwa tana 'daki tana bacci.

Kallon sa'adah tayi tace,
Maman abdul bakida 'kanwa ko wata dakika san ta iya komai kamar ke kikawomin ina tsananin bukatar me aiki gaskia kuma xan  bada  ko nawa takeso indai har tanada tsafta kuma ta iya aiki.

Babu wadda tafadowa sa'adah arai sai nazli dan tasan tama fita iya aiki da tsafta.
To amma yazatayi da waleed dan tasan naxli bazata iya rabuwa da waleed ba daidai da minti 'daya bare taje har abuja tabarshi amma xata gwada tagani.
Cikin jin dadi tace,
Akwai 'kanwata kuwa tana gida ta ta'ba aure mijin ya 'bata tanada 'da 'daya kuma tanada tsafta fiye danima.
Farin ciki fal fuskar fannah tace,

Yauwa maman abdul kije gidan kijiyo idan zatayi aikin saiku taho tare sbd saura kwana biyar mu koma.
Meenah data fito 'daki cikin wata 'bingilalliyar riga ta xauna tana tambayar firar me sukeyi.
Fannah tayi mata bayani nan itama tayi naam da hakan tunda dan kula da 'bangaren rabin rantane wanda tuni fannah tasan son da meenah kewa tameer kuma tamata alkawarin ganin ya aureta insha allah.

🌕🌕👉
🌕⚜️DA'IMAN⚜️🌕

Na

MAMUH GEEE

☆dedicated to☆
Husnah bbchoudiallo

136→140

Zaune suke atsakar gidan inna na bubbuga 'dan redionta daya tsaya kwana biyu waleed na kwance jikinta yana wasa da zaren tabarma
Ita kuwa tanka'den gari take ahankali tayi nisa cikin tunani.

Sallamar sa'adah tasa dukkaninsu 'dagowa suna kallonta cikin farin ciki banda nazli datayi nisa cikin tunani.

Harsuka gaisa ta zauna inna na tambayarsu abdl data baro nazli batasan me ake ciki ba.

Cikin tausayi da jimami sa'ada takalleta tamaido da kallonta ga inna tayi mata bayanin aikin data samowa nazli ta 'dora da fadin,
Inna ina ganin kodan asamu ta rage wannan damuwar datake ciki ta 'bacewar abban waleed kuma tasamu tasaka waleed makaranta kodan yanayin rayuwa.

Jinjina kai inna tayi cikin gamsuwa da zancen sa'dah amma kuma zaiyi wuya ita nazli ta yarda

sbd baxata taba 'yarda tabar waleed ba.
Cikin jinjina kai tace,
Kinsanfa nazli waleed da tameer sune rayuwarta
To tarasa tameer yaya kike ganin xata iya barin waleed dan yanxu ko nan da 'kofar gida bata bari yafita wasa.

Waleed ne yafada jikinta da 'karfi yana cewa,
Anty ki goyani.

Dawowa tayi daga dogon tunanin data fada sai kawai taga sa'adah zaune da inna
Ta saki fuska tana cewa,
Anty sa'adah yanxu kike tafe,
Ya hanya?
Inasu abdul?

Cikin sakin fuska ta amsa tana cewa,
Nazli bazaki hakura ki fawwalawa allah komaiba kullum sai 'karewa kike kinsa tunani aranki fiyeda shekara nawa.

Murmushin 'karfin hali tasaki tana danne hawayenta.
Inna ta gyara xama ta zayyanewa nazli abunda yakawo sa'adah.

Shiru tayi cikin tsananin tashin hnkli amma kuma batajin zata iya watsawa inna da anty sa'adah ido sbd sun taimaketa fiyeda tunani
To amma kuma waleed 'dinta fa?

Anty sa'dah ce ta katse mata tunani da cewa,
Nazli nasan waleed kike tunani
To kadaki damu zamu dashi kanon saiki barsa agurina asakasa mkrntar dasu abdl keyi ta gwamnati.

Shiru tayi tana 'boye hawayenta na tsananin tausayin kanta da 'danta.
Inna tace,
Nazli kadaki saka damuwa aranki wannan ba abun damuwa bane idan bakyason zuwa baida matsala munsan halinda kikeji.

Share hawayenta tayi tareda rintse ido tace,
Inna tunda har anty ta tunada ni ta nuna kulawarta akaina ta taso tazo bazanji dadi ba idan har nayi mata haka dan haka inna inkinyi na'am zanje.

Aa nazli kiyi tunani ba abun takura bane.
Bakomai inna aitunda aikin na 'dan lokacine tace kuma idan naje naga ba matsala aisaina dawo

natafi da waleed 'din kuma aiba tabbata zanyi ba.

Sosai suka jinjinawa yanda ta daure tayi musu bazata dan basuyi tunanin zata yarda haka da wuri ba.

Harta gama aikinta dare yayi suka kwanta akan gobe zasu wuce hawaye take tanajin wani irin sabon ciwon 'batan tameer 'dinta dakuma jin cewar abj za'a da ita
Garin da takejin tsanar shigarsa ayanxu sbd ba tameer 'dinta.

Har gari ya waye tayi sallah goge hawaye take.

Saida rana suka fito dan tafiya sai alokacin tasaki siririn kuka
Inna da itama takejin damuwar kewarsu dazasuyi ta lallasheta suka wuce.

Da maraice suka isa gidan me gidanta dake zaune bakin gate na ganinsu yataso yana musu sannu harsuka shige boys quatrs inda anan suke zaune.

Sallah sukayi sukaci abinci nan waleed yafara wasa dasu abdl duk da sun girmesa.

Sai bayan sallar magrib taja nazli 'din suka nufi sashen mutanen gidan dan gabatarda naxli ga fannah.

Zaune suke dukkaninsu a palon suna fira idan kacire fannah dake 'daki tana waya dasu ammah daga cairo.

Cikin ladabi sa'adah ta gaidasu
Amsawa sukayi suna kallon nazli dake tsaye gefenta sunne dakai.

🌕🌕👉mamuh geee
🌕⚜️DA'IMAN⚜️🌕

Na

MAMUH GEEE

☆dedicated to☆
Husnah bbchoudiallo

141→145

Haj wanannan ita 'kanwata da haj fannah tace nasamo mata yar aiki.
Kai sunkuye nazli ta gaidasu suka amsa batareda sun 'kara kallon gefentaba.

'Dakinda fannah take can sa'adah ta nufa nazli na bayanta jiki duk amace.

Tura 'kofar 'dakin tayi tareda sallama tashiga suka tsaya nazli na bayanta har lokacin kanta aduke yake.

Ganinsu yasa tacewa ammah dasuke waya, granny i will call you later inada ba'ki.

Kallon sa'adah tayi tana murmushi tace,
Maman abdul sannu da dawowa wanban itace 'kanwar taki? Tafa'da tana kallon nazli.

Eh itace gatanan nace muzo ki ganta.

'Dagowa nazli tayi zasu gaisa
wani mahaukacin bugu xuciyarta tayi
Tari mai 'karfi ya sar'keta su duka sukayo kanta fannah tayi saurin bata ruwan swan dake kan bedside drower.

Kasa karbar ruwan tayi ta dafe zuciyarta dake bugawa da 'karfi kamar xata faso ta watse.
Kallon tashin hankali takebin fannah dashi
Saida sa'adah ta jijjigata da 'karfi ta'dan sauke idanunta 'kasa.
Tameer,waleed dakuma wannan budurwar yarinyar komai nasu zak babu banbanci kamar 'yan uku.
Tabbas datasan tameer 'dinta nada 'kanwa to da saitace wannan 'kanwarsace,
Hakama dah ba ita ta haifi waleed ba to dah tabbas saitace wannan itace ta haifesa.
Yawu ta hade dakyar ta gaidata
Fannah tasaki ajiyar zuciya tana cewa,
Ohh wlh ni harna tsorata.

Kallon nazli tayi tsaf taga tabbas babu alamar 'kazanta atareda ita saidai talauci daya

koma'data.
Gata budurwa kamarta kamar bata haihuba dan badan sa'adah dakanta tace mata ta haihuba da vazata yardaba.
Gata Kyakkyawa sosai kamar itama balarabiyarce duk da ta dafe ta 'kanjame hakan hana fannah gano hakanba dan tayi mamakin sam ba xubinsu 'daya da maman abdl ba.

Shikenan maman abdl tayi ba matsala saikuje tun anan ki kokkoya mata wasu abubuwan kafin jibi xamu wuce kuma zan ringa bata dubu talatin a wata.

😳zaro ido sa'adah tayi itakuwa nazli bata wani damuba dan babu wani abu dayake burgeta ko aikin zatayine kawai sbd zuciyarta dake ingixata takuma rasa gane meyasa.

Godiya sukayi suka fice suka koma can gurinsu sa'adah.

*********
Washe gari duk aikin gidan tare sukayisa sa'adah na bata shawarar iya xama da mutane.

Sam su haj karima da haj bilki babu wanda yagane nazli ko kusa sbd muguwar canxawar datayi sannan kuma dama can ba wani cika ganinta sukayiba tunda kullum tana sama.

Sun fara hidimar bikin daya kawosu dan gobene xaa daura aure amarya ta tare kowa ya watse.

Sosai fannah ta fara yabawa da halin nazli sbd yarinyar akwai nutsuwa da tsafta ga wani irin class datake dashi duk da tana 'yar aiki dan bata shiga lamarin kowa saina ita data 'dauketa aiki.
Murmushi tayi tana cewa,
B nasan zakaji dadin wannan abun danayi mana tunda nasan sarai kana bu'katar mai kulada tsaftar part 'dinka dan nafisat aikin yayi mata yawa da bazata iyayinsa yanda kakesoba.

Ranar dazasu wuce kuka take wiwi akan rabuwa da waleed amma haka tayi masa wayo suka fice.

Aharabar gidan ta tarar dasu sun fito suka shiga mota akayi airport dasu.

Jirgi suka shiga babu bata lokaci suka 'daga xuwa abuja.

Da maraice suka isa motar gidan haj bilki tazo 'daukarta
Itama haj karima direbanta yazo 'daukarta.
Suma motarce tameer ya aiko 'daukarta airport.

Suna isa gidan kai tsaye 'dakinta ta wuce nazli na biye da ita sbd babu kowa a gidan
Dad baya 'kasar yayi tafiya,
Tameer ma bayanan yaje lagos meeting hakama mum tana cikin gari sai dare zata dawo.

Akwatinta da nazli ta jawo mata tayi mata nuni data shigar dashi bedroom.
Kaiwa tayi tadawo ta tsaya gefe atsaye bakomai hannunta dan fannah tace kada tadauko kayanta zata siya mata kaya idan sunzo nan 'din dan idan b 'dinta yaganta a yamutse zai iya cewa bayason aikinta dan bayason 'kazanta ko ka'dan.

Nafisa fannah takira da landline 'din palonta tace tazo yanxu tana nemanta.

MUCH LOVE😍😍😍😍😍😘😘😘😘😘

🌕🌕👉mamuh geee
🌕⚜️DA'IMAN⚜🌕

Na

MAMUH GEEE

☆dedicated to☆
Husnah bbchoudiallo

146→150

Turo 'kofar palon fannah 'din tayi tareda sallama ta 'karaso kusada nazli ta tsaya tareda cewa,
Gani.

Hankalinta nakan wayarta Tana 'kakarin kiran b 'dinta tace,

Nafisa wannan wadda zata ringa kula da tsaftar dakina da palona dana b ce kuma ni takewa aiki ba kowa ba atakaice komai nawa dana b
Is her responsibility ta kula dashi.
Daidai nan tameer yadau wayar ta mike tayi 'daki tana waya dashi.

Atsanake suka juyo dan gaisawa da juna
Lokaci 'daya kamar wa inda wutar lantarki taja kowanne yaja baya da sauri cikin mugun tsananin ki'dima.

Nafisa ce tayi 'karfin halin 'daga hannu tana nunin nazli 'din tana cewa,
Nazli kece?
Ko kuwa idanuna ne?

Nazli datafi firgita sosai dan nan take tafara tunanin kaddai fannah 'yar uwar tameer ce takawota gidan aiki?
Idan kuwa hakane kiketa zasuyi saita kaisu gurin tameer
Tameer 'din dabatasan inda yakeba
Yanacan 'kilama cikin mugun garari.

Girgixata nafisa tayi da 'karfi jikinta na rawa ganin sai zubar hawaye take ba magana.

Murya na rawa cikeda damuwa da tsoro tace,

Nafisa inane nan?
Ina haj xeenat?
Wacece wannan fannah 'din?
Wane gidane nan?

Duk arude take watsowa nafisa tambayoyin
Itama nafisar arude take
Kawai saita damki hannun nazli tajata sukabar palon.

'Dakinta dake gurin 'kofar kicin tajata ciki ta dannawa 'kofar key har alokacin duka hankalinsu atashe yake su duka.

Jiyowa nafisa tayi a kidime take cewa,

Nazli nan ba gidan kowa bane face gidan alh zaid da iyalansa,

Haj zeenat nanan acikin gidan,

Sun baro can gidan sun dawo nan ne tun bayan da alh zaid yadawo yatarar da 'bacewarku yakasa zama awancen gidan,

Fannah 'kanwar sir tameer ce daya dawo da ita nan tun bayan dawowarsa daya samu lapiya.

Tunda nafisa tafara koro mata bayanan hankalinta da nutsuwarta suka fara barin jikinta amma Kalmar nafisa ta 'karshe ita tafi dukan zuciyarta ta razanar da ita fiyeda tunani.

Kamar bebiya tafara nuni da hannu tana cewa,
Meer...meer...a..a...ina
Meer...ya...ya...

Ganin takasa 'karasawa dan a birkice take yasa nafisa ta gya'da kai tace,
Tabbas nazli sir tameer ya warke yanzu yana cikin cikiakkiyar nutsuwarsa.
Dr ibrhm yakira alhaji yace ya bugesa da mota can hanyar wani 'kauye a kano
Akayi kasar waje dashi kuma yana farfadowa cikin hankalinsa yatashi wanda kowa yayi mamakin hakan.

Nazli babban abun ba'kin cikin dazan fada miki yanxu shine
SIR TAMEER BAISAN KOMAI DAYA FARU LOKACIN RASHIN LAFIYARSA BA ma'ana BAISAN DAKEBA BAZAI TINAKI BA.

Sulalewa tayi 'kasa tana neman shi'dewa komai na duniyar na juya mata
Jitake kamar zuciyarta zata buga
Gaba 'daya zantukan nafisa sun hargitsata batamasan wane tunani zatayi ba.

Sai alokacin wani irin kuka mai ciwo yazo mata ta 'kankame jikinta tanayi abunta sosai.
Yanda take kukan ne ya masifar kashe jikin nafisa dan tana tunanin akwai abunda yafaru akan rabuwarsu.

Zama tayi kusada ita tanason ta rarrasheta amma yanda nazli ke kukan tana bukatar abarta tayi abunta kodan samun saukin radadin zuciya sbd kalar kukanta ya bayyana zuciyarta tana cikin wani mugun hali.

Tsoro nafisa tafaraji ganin nazli na neman sha'kewa ahalinda take ciki
Ta dafata cikin tausayi tana shirin yin magana nazli ta gwalo mata manyan idanunta dasukayi jajir sbd kuka.
Girgixa kai tayi murya ashake tace,
Dan allah ki fitar dani agidan nan yanxu,
Banason bayanke dakika ganni wani yaganni musamman haj xeenat
Bakuma zan iya jurar ganin meer 'dina yaganni amma baisanniba,
Bai tunaniba,
'Karshema yanamun kallon 'yar aiki
Baxan iya jure wannan ba
Gwara natafi nakoma nayi jinyar xuciyata dazata rayu da tsananin sonsa da damuwar rashinsa

'karshe ta mutu da sonsa.

Nazli kece wadda duk masoyan alh da 'yayansa ke adduar su samu sbd nagani nakuma ji ajikina kece zaki kubutar dasu daga sharrin hajiya.

Mikewa tayi tana nufar 'kofa nafisa tayi saurin shan gabanta tace,
Nazli ina cikin jikinki dakika tafi dashi?

Cikin kuka tace,
Babushi ya xube.

Garin yaya yazube?
Bansaniba nima

Tun yaushe?
Bazan iya tunawaba

Bazai yiyu ba sbd kinason tameer nasani fiyeda kanki dan haka joda cikinsa dake jikinki ya zube nasan bazaki taba manta ranar ba.
Dan haka tun yaushe ne cikin ya zube?

Shekara hudu. Tafada da 'karfi tana kuka dan duk tambayoyin na nafisa a jere take matasu duk sun rudata dan dama aruden take.

Ja baya nafisa tayi tareda sakin ajiyar zuciya tace,
Shekarar abunda kika haifa hudu kenan nazli
Dan banyarda da cikin yafitaba.

Rintse idanu tayi tana jingina da bango hawayenta naci gaba da ambaliya.
Gidan takeson bari danji take makar zata 'kone tsabar ciwon zuciya.

Cikin hawaye da sanyin murya tafadawa nafisa komai tun bayan barinsu gidan 'karshe ta 'dora da fadin,
Rayuwata ba 'daya daga cikinsu wato meer ko waleed to tabbas batada amfani agareni.
Inasonsu fiyeda kaina,
Inason meer tun bansan soba,
Inason duk wani abu daya dangaci meer 'dina shiyasa nakeson waleed fiyeda numfashi sbd duk nakallesa fuskar meer da jinin meee nake gani yana yawo ajikinsa.
Inason meer 'dina,
Inason meer 'dina kuma meer 'dina yana sona kaman yanda nake sonsa
Amma wannan na yanzu ba meer 'dina bane sbd meer 'dina bazai mantani ba,
Bazai daina sonaba,

Meer 'dina ya mutu ya barni daga yanzu zanyi takabar meer 'dina
Nida waleed 'dina munzama marayu mun rasa meer 'dinmu wannan tameer ne yafi 'karfinmu.

Kukan tausayinta nafisa keyi tana lallashinta.

🌕🌕👉mamuh gee
🌕⚜️DA'IMAN⚜️🌕

Na

MAMUH GEEE

☆dedicated to☆
Husnah bbchoudiallo

151→155

Kiranta fannah tayi ta hanyar landline 'din 'dakin nafisa
Nafisa tafada mata suka mike gaba 'daya zuwa can 'din.

Kaya dake gibge kan kujera ta nuna mata tareda cewa,
Ki 'dauka ga kayanan zan siya miki wasuma sbd inaso ki ringa wanka biyu ayini tareda canza kaya dan ki kasance atsaftace koyaushe.
Na yaba da tsaftarki amma inaso ki 'kara dan kiyaye duk abunda zai 'bata ran b 'dina.

Ki gyara 'dakina yanzu bari ni nashiga wanka.
Bedroom tashige tana tubewa tashige toilet.

Nafisa ta kwasar mata kayan sta fice itakuma ta gyare gurin cikin sanyin jiki.
Tana gamawa ta fito kenan yayi daidai dashigowar haj xeenata dasu haj karima harsun samu

fitowa daga dawowarsu dan bata rahoton gurin boka dasukaje can kanon.

Zabura tayi da 'karfi taja baya tana nuna nazli tareda ha'de wasu wahalallun miyau.

Kallon rashin fahimta suke mata haj bilki takalli nazli tamaido da kallonta ga haj xeenat tace,
Me aikin da fannah ce datasa aka samo mata tun akano fa.

Afirgice takallesu tace,
Kun kuwasan me kukayi barin wannan tsinanniyar tazo mana da wannan
Ta nuna nazli a rude.

Haj karima tace,
Xeenatu kiyi mana gwari gwari mana munkasa gane me kike nufi.

Karima nazli ce fa matar shegen tsinannen yaron nan.
Meyasa kuka bari tazo da ita?
Na shiga uku ni zeenatu meyasa abubuwa ke neman tabarbaremun ne?

A kidime suke kallon nazli datati 'kasa da kai tana adduar allah yasa su koreta yanzu basai gobeba tabar gidan dan tabbas bazata iya rayuwa agida 'daya da tameer ba.

Wata wawuyar dam'ka haj xeenat takai mata ta shaqota tana fadin,
Zo tsinanniya munafuka kibar gidannan yanxu tun wani daga cikin alh ko tameer basu gankiba duk da nasan yanxu baisankiba ko kukuwa wlh nayi miki mummunar kisa.

Janta tafara tanajin wata irin tsanarta kamar ta shaqeta ta mutu ta huta.

Riqeta haj bilki tayi da sauri tana ha'da zufa tace,
Aa wannan ba itace mafitaba agaremuba dan taga inda suke yanxu zata iya dawowa ta baya ta tona asirin komai ta gudu kuma kunga basanin inda takeba zamuyi bare mu 'dau fansa ko mataki akanta.

A ru'de haj xeenat tace,
To meye abinyi dan namatsu tun kafin shegiyar can ta fito taganmu ahaka tayi zargin wani abin.

Haj kareema tace,
Mafita 'dayace mu barta anan muna ganin duk wani motsinta da abunda takeyi duk ranar data gudu ko ta tona mana asiri wallahi saimun bashi guba ya mutu tunda shine abunda tafi so fiyeda komai tunda allah ma yasa babu shegen cikinta dayanzu masifar dazamu shiga saitafi haka.

Jinjina kai sukayi cikin gamsuwa da bayaninta haj xeenat ta 'dora da fa'din,
Kuma duk rintsi kadaki bari alh yaganki kuma kadaki bari tsautsayi yasa ki nuna kinta'ba

ganinmu arayuwarki dan kuwa da kaina zan dama guba na basa kina kallo yasha,
Bake bashi,
Ki tsaya amatsayinki na me aikinsa da tsinanniyar qanwarsa.
Idan kikayi ganganci to kisani da rayuwarsa kike wasa dan yanzu tana hannunki.

Ficewa sukayi batareda sun tattauna abunda yakawosuba.

Kukandata risga adaren bai fa'duwa sbd abun yazo mata ba yanda tasoba.
Meyasa koyaushe tameer ne abunda kowa ke amfani dashi gurin quntatar da ita?
Meyasa tameer yazama wanda zata iyayin komai akansa har ayanzu dasuka zama duniya daban daban?
Tameer shine farin cikinta,
Shine baqin cikinta,
Shine damuwarta,
Shine buqatarta.
Kuma shine weak point 'dinta.
Yanzu gashi once again zatayi rayuwar wulakanci acikinsu akansa duk da baimasan tanayiba.
Amma koba komai zata zauna tayi gadin
Koda garin haka zata rasa rantane.

Koda garin ya waye fuskarta ta kumbura suntum ko gani sosai batayi amna haka taje tayi gyaran dakin fannah tsaf.

********
Sannu ahankali ta 'dan saba da fannah sbd tana janta ajiki sosai tana kula da ita kamarba 'yar aiki ba.
Wasu lokutan kiranta take su zauna tana janta fira duk da ita bata sakewa sosai.

Abunda ta lura dashi shine tana tsananin son yayanta sbd takanas ta 'dauketa takaita shago tayo mata siyayyar turaka masu kyau da qamshi da kaya sosai duk dan sbd kada yayanta shaki wari ko tsami  idan tana masa aiki.

Itadai damuwarta duk kayan yawancinsu dogayen rigunan kantine masu kyau da 'dan kama jiki.
Amma haka take sakawa atakure tana aikin.

'Bangarensu haj xeenat kuwa ido sosai suka saka akanta.

⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜

Duk inda nutsuwarta take bata jikinta yau dan yau tameer zai dawo
Tun safe aka bu'de mata sashensa amma takasa shiga ta gyara saida nafisa takama hannunta suka hau saman har cikin tsakiyar palonsa kafin ta juya ta fita.

Lumshe idanu tayi tana tsiyayar hawaye.
Komai na palon tsaf yake sai 'kamshi dake tashi duk da 'dakin ya kwana biyu bakowa.

Daqyar ta lalla'ba kanta ta gyara palon da bedroom ta fesheshi da airfreshner masu da'di ta kukkuna ac ta rufo qofar ta fice.

Girki na musamman sukayi hadda fannah 'din sai farin ciki take ga aminiyarta meenah tuni ta iso taci wani irin ado dan tarbar tavin ranta.

Suna gamawa suka jere a dining fannah tayi gurin wanka bayan ta umarceta da itama taje tayi wankan dan driver yaje 'daukarsa daga airport.

🌕🌕👉mamuh geee
🌕⚜DA'IMAN⚜🌕

Na

MAMUH GEEE

☆dedicated to☆
Husnah bbchoudiallo

161→165

Cikin rashin bawa xancen mahimmanci yace,
Tunda kunaso zan duba nagani.

Mikewa yayi yabar gurin yana xuba hannuwa a aljihun wandonsa.

Dai dai xai shiga 'dakin ita kuma ta fito 'daukeda glass cup din fresh milk sukayi wani wawan karo
Fresh milk 'din tazube ajikinsu gaba 'daya tayi baya da qarfi cikin tsoro aikuwa ta taka wadda ta xuba a qasa santsin tiles yayi mata mummunan ja ta tafi da qarfi zata xube
Wata fixga yay mata ta fado masa da qarfi saikuma suka zube gaba 'daya.

Fannah dake tsaye ta dariya ta kufce mata dan tun qarar faduwar cup 'din ta taso dan dubawa komai akan idonta yafaru.

Dariya take sosai kamar 'yar bby sbd ganin yayanta kwance cikin madara har a fuskarsa ga nazli itama duk ta 6aci da madarar sai suka koma kamar wasu yara.

Saurin tashi tayi daga jikinsa ta bar gurin da sauri idonta na qoqarin kawo ruwa dan haduwar jikinsu ya zaburo mata da tsimin sonsa datake neman dannewa.

Mikewa yayi yana ha'de fuska yayi hanyar stairs dinsa.
Gaban madubin bedroom 'dinsa ya tsaya sai kwai yasaki murmushi dan komawa yayi kamar yaron da yayi 'banna.

Wanka yayi yayi sallar magrib yazauna palon yakira  fannah.

Da sallama tashigo palon itama ta canxa kaya tana 'daukeda tray 'din farfesun kifi da akayi masa fannah na bayanta.
Ajewa tayi tana mikewa fannah tace,
Nazli ki xuba masa saiki 'dauko ruwa da drinks ki kawo masa.

Riko hannunsa tayi tace,
B pls get married,
I really want to see you happy kuma inason naga 'yan babys sun fara kirana aunt.
B pls do dis for me qnd marry my friend meenah.
Na yaba maka da ita and you knw i always choose wats best for you.
She's very nice,
Kind and gud..bayan wannan she really loves you.

Kallon tv yake yana saurarenta jin muryarta ta fara rawa kaman xatayi kuka yasa ya juyo aikuwa hawayen take
Jawota yayi jikinsa yana cewa,
Little youre askin for sumtin dat i dnt really tink i can do for you.
Marriage is not a joke or sumtin simple.
Its abt my future,my happiness my.....

Daz y i want you to get married b bcos i want to see u live a happy life..
Pls pls b do this for me,
Do this for ur little sister.

Zanyi tunani little but for now pls kibar xancen okey?
Kai ta 'daga cikin tana murmushi.

Miqewa tayi xuciyarta na bugawa da qarfi kamar zata fashe.
Kishinsa takeji yana kona zuciyarta ta fice da sauri tabar palon ko ruwanma bata 'dauko masaba sai dai fannah ta kawo masa.

Sosai ya lura da yanayin data shiga amma ya basar sbd baisan dalilin shigarta halinba.

Kuka ta la6e ta risga a 'daki har saida taji kanta na sarawa kafin ta lallashi kanta ta fito.

Da daddare harta kwanta fannah takira wayarta data siya mata dan irin haka.

Nazli pls ki kaiwa b hot coffee yanxu yanacan yana jira.

Kicin ta nufa ta 'dora yanayi ta juye tadauka ta nufi 'dakinsa.

Apalo ta tarar dashi zaune da farar singlet da farin dogon wandon bacci mai taushi yana aiki da laptop.

Duqawa tayi ta aje tray 'din akan center table 'din dake gabansa,
Qamshin turarenta ya daki hancinsa ya lumshe ido batareda yakalli gefen datake ba.

Mikewa tayi zata fice saitaji tanason kallon fuskarsa ta juyo ahankali idonta tab da hawaye.
Juyowarta tayi daidai da 'dagowarsa idanunsu suka shiga cikin na juna.

Qurawa juna idanu sukayi
Tsantsar damuwa yake hangowa a idanunta yayinda ita kuma take hango rayuwarta a idanunsa.

Hawayene suka gangaro mata ta juya da gudu ta fice tana toshe bakinta sbd kukan dayazo mata.

Qofar yabi da ido cikeda mamaki
Dan iya tunaninsa magana bata taba shiga tsakaninsu ba amma yanayin yanda ta kallesa kamar tasanshi yayi mata wani laifi.

Shafo fuskarsa yayi yana ayyanawa aransa akwai wata damuwa atare da ita.

**********
Bayan 'dan lokaci ya amince da maganar auren meenah badan yana sonta ba sai dan yanda fannah ta damu sosai akan zancen dan shi sam beyi wani tunanin xai iya samun lokacin kula mace bare soyayya ayyukan gabansa ma kawai sun ishesa arayuwa.

Meenah,haj xeenat,haj kareema,haj bilki da fannah ji suke kamar su taka kan jariri sbd farin ciki, tuni aka fara shirin biki sbd har dad yazo ankai qarshen komai.
meenah tuni ta dawo gudan da xama dan idan ba ita ta nemesaba baya bi takan zancenta saiya xama itake zuwa fira 'dakinsa.

🌕🌕👉mamuh geee
🌕⚜️DA'IMAN⚜🌕

Na

MAMUH GEEE

☆dedicated to☆
Husnah bbchoudiallo

166→170

Zaune suke a garden 'din gidan yana waya dasu ammah akan sha'anin bikin yace suyi zamansu basai sunxo ba bayan bikin zasuzo tareda meenah 'din.

Meenah dake zaune taredashi tasaki wani murmushin farin cikin samun cikar burinta dan yanda takeji ko kisa xata iya akan tasamu tameer.

Miqewa yayi sbd umminsa haj nurat data karbi wayar zasuyi magana kasancewar yasan

batason auren da meenah yasa yatashi ya zagaya yana wayar 'dayan hannunsa na sanye cikin aljihun 3quater jins blue dake jikinsa da farar body hug.

Yana cikin yin wayarne yaringa jiyo sheshshekar kuka natashi ahankali.
Ignoring yayi yana cigaba da wayarsa.

Sautin kukan yafara yawo a kunnuwansa har baya iya fahimtar me umminsa ke cewa,
Ya rintse idanunsa yanason kukan yadaina damunsa amma ina saima qara shigarsa yake haryana dukan zuciyarsa.

Bayan flowers 'din gurin ya nufa sbd daga can kukan ke fitowa.

Duqe take tasaka kai atsakiyar qafafunta tana rero kukan.
Bayanta ya kalla ya gane 'yar aikin nance. Juyawa yayi yana 'bata fuska yana jin haushinta aransa na yanda takeda damuwa takasa fa'da ataimaka mata tunda tasan fannah zata iya taimaka mata da koma nawane.

Cak ya tsaya xuciyarsa na tantama sbd sunansa dayaji ta fa'da cikin kuka.

Tameer,meer meyasa rayuwata take wahala haryanxu akanka?
Meyasa zan zauna dan ganin wannan baqar rana agareni duk dakai farin cikine agurinka.
Waleed 'dina zai tabbata a maraya kenan shima baqar rayuwar danayi ita xaiyi sbd rashin mahai....
Bata qarasaba kukanta yaci qarfinta duk da bata bari sautinsa yafuta ba.

Xuru yayi qwaqwalwarsa a cunkushe dan baisan tunanin dazaiyiba.
Baimasan me zancen nata yake nufiba,
To amma meyasa sunansa yashiga zancen nata?
Kodai bashi tameer 'din ba.
And waleed?
Who is that waleed she's talkin abt?
Is he her hus...

Juyawa yayi yabar gurin dan tuni kansa ya fara sara masa.
Baikoma takan meenah ba yawuce 'daki kai tsaye.

Da daddare data kawo masa fresh milk ko kallonta baiyiba sbd bayason yaringa damun kansa da abubuwan daba serious ba.

Juyawa tayi ta fice jiki asanyaye kamar mara lafiya.

Bayan ta fita saiyaji yana buqatar coffee sai bai nemi fannah ta turo masa ita ya miqe yasauko

dakansa dan yasa nafisa tayi masa sbd ita 'din ya lura kaman tana cikin tough time.

Ba kowa apalon dan haka ya nufi qofar 'dakin dan qwanqwasawa
Hannu ya 'daga zai buga maganar nafisa ta daki kunnansa,

Nazli pls kadaki bari ayi wannan auren ki fito ki fa'da komai
Ki bayyana musu waleed da gaskia sbd da anyi wannan auren babu wata mafita dan kuwa burinsu yagama cika akansu.
Kuma dolene sir yasan gaskia wata rana dan haka gwara ki sanar ma......

Cikin tsananin kuka tace,
Nafisa babu gurina arayuwarsa yanxu,
Yana cikin farin cikinsa bazan katse masashiba dan tarayyata dashi ba abunda yaja masa sai wahalar rayuwa da qasqantacciyar wahala.

Kasa sauraron sauran yayi yajuya yabar qofar
'Daki yakoma yakasa zama ya kasa tsayuwa so yake ya gano me suke nufi amma bai ganoba qarshema ciwo kansa yafara saiya kwanta kawai.

Tundaga lokacin yafara saka ido akanta sbd hankalinsa ya kasa kwanciya akan xancensu duk da yanada tabbacin wani tameer ne suke magana akai.

**************
An fara shagalin biki sosai dan dukiya alh zaida da tameer suka sake musu anata shagali duk da dad bai dawoba sai saura kwana 'daya 'daura auren.

Shagali sukeyi sosai duk da angon baida lokacinsu saisu ka'dai suke bidirinsu sudai suga an 'daura auren.

Duk iya yanda ta kama kanta sosai ta danne xuciyarta hakan bata faruba sbd muguwar rama tayi sbd tsananin damuwa da tunani dan yanxu kukanma ya daina zuwa saidai idanuwanta su ka'da suyi jajir.
Fannah da kanta tasata agaba tace nazli bakida lafiyane ko kinada damuwar zama damune?
Kai kawai ta girgixa mata.
Kula da abincinsa yana kanta dan tun fara biki fannah take jaddada mata hakan.

Toilet 'dinsa take wankewa cikin cikin tsautsayi bakin taje kunna tab saita kunna shower aiko ruwan sukaxo da qarfi nan take suka jiqata jagab.
Dan qaramin tsaki rana kallon yanda ta jiqe gaba 'daya har gashinta.

Sanin bayanan bakuma kuma baya dawowa sai maraice yasa ta
Xame hijab 'dinta ta shanya a toilet din hakama doguwar rigarta danso take kafin tagama sun 'dansha iska.
Bra ce fara qal ajikinta da farin under skirt tsaf dasu kamar sabi sbd sosai fannah ke siya mata duk wani abun buqata.

Zaune yake a sit 'din baya yana sanye da suit black masu red tie sai qamshi yake zubawa driver na tuqasa.
Wayarsace tayi qara ya duba saiyaga p.a 'dinsane cikin qasaita ya 'daga wayar.
P.a dinsa yace,
Sir am sorry walh meeting 'dinnan sun aiko wai sunada babban uxuri an 'daga sai gobe kuma.

Kasa magana yayi sbd haushi sai kawai ya datse kiran ya kashe wayoyinsa gaba 'daya yace driver yamaidashi gida yama fasa xuwa office 'din yau gaba 'daya.

A gate 'din farko yace driver ya ajesa ya aikesa office shikuma ya taka ya 'karasa wanda hakan ya hana sam tasan da yadawo.

Dai dai qofar shigowa palon yaci karo da fannah tana riqeda coke ahannunta tanasha zata fita cikin sauri dan xuwa gidansu meenah sbd yaune suke qunshi.

Gaba 'daya coke 'din ta 6atasa
Ya rintse idanu cikin takaici kafin ya wuce da sauri yana ce mata ta tafi kawai tunda yaga she's in hurry.

Yana shiga palonsa yasawa qofar key dan bayason adamesa wanka kawai xaiyi ya huta.

🌕🌕👉mamuh geee
🌕⚜️DA'IMAN⚜🌕

Na

MAMUH GEEE

☆dedicated to☆
Husnah bbchoudiallo

171→175

Yana shiga bedroom 'din ya kalli jikinsa yana 'dan yamutsa fuska dan yaso yana dawowa ya kwanta ya huta amma yanxu saiya kuma wani wankan.

Tu6ewa yayi ya 'daura farin towel a qugunsa kyakkyawan jikinsa da lafiyayyar fatarsa sai sheqi suke alamar hutu daya ratsasu.

Kai tsaye ya bude qofar toilet 'din yashiga tareda rufowa.

A firgice ta 'dago daga duqen datake tana canxa ruwan cikin bathtub.

"Ohh my god" ya fa'da yana kare idanuwansa da hannunsa cikin wani irin tsoro da ganin dirinta daya kusan tafiya da numfashinsa dan nan take yaji wata sha'awa ta taso masa.

Gabaki 'daya rikicewa tayi tama rasa yazatayi ta fito dan wani santsi ke janta yana maida ita tama kasa fitowa bare takai gurin kayanta.

Jin tasaka fitowa sai zamewa take yasashi matsowa ya miqa mata hannunsa danshi amatse yake data fice dan ya rikitu sosai ga qamshin turarenta daya cika gurin.

Qaf qaf tafara da idanu tana sake qoqarin fitowa batareda takama hannun nasaba.

Zamewa tasakeyi shisaima tabashi daria ya saka hannuwansa biyu ya 'daukota gaba 'daya aiko bai qarasa fitowa da itaba santsi yajasu gaba 'daya suka fa'da cikin bathtub 'din hannunsa ya bugi shower saiko ta fara sako musu ruwa.

Itace a qasa shine asamanta jikinsu ya ha'de sosai gashi babu me kaya ajiki acikinsu
Nan take suka shiga wani yanayi sbd body contact dasuka samu.

Qurawa juna idanu sukayi basako qyaftawa duk da ruwan shower dake xuba akansu.

Hannu yasa ahankali ya matsar da dogon gashinta daya jiqe ya 'dan hawo gefen fuskarta.

Cikin wani salo ya janye da gashin yana kallon tsakiyar idanunta.

Shafo gefen fuskarta yayi har xuwa wuyanta cikin wani salo
Taja numfashi ahankali tareda lumshe ido.
Kasa bude idonta tayi sbd fuskarsa dataji tana matsowa xuwa tata.
Da sauri numfashinta ke fita har qirjinta na 'dagawa yana komawa.

Qirjin ya qurawa ido hankalinsa na qara ficewa daga jikinsa sbd ganinsu farare tas acike tsaye acikin bra 'dinta suna daqawa suna koma sbd numfashinta dake ja.

Hannu yakai ahankali ya shafosu cikin wani salo ai 'dauke huta tayi ta bude baki numfashinta na fita ahankali ya maida kallonsa ga 'dan bakinta bai tsaya komaiba ya shigar da nasa cikin nata 'din.

Ahankali yake kissing 'dinta yana qarajin wata fitinanniyar sha'awa na taso masa.

Zare bra 'dinta yayi yana ya jefar yana qara cusa bakinsa anata.

Sam basusan me sukeba dan kuwa tuni alamari yayi nisa.
Qoqarin rabata da pant 'dun jikinta yake ta dawo hayyacinta
A furgice ta zame tareda sakin kuka ahankali.

Dafe kansa yayi cikin tsananin kunya da takaici
Dan baisan meya hau kansa yatashi aikata hakaba.

Dukkaninsu kasa motsi sukayi sbd rashin kuxari
Ita kuwa harda kunyar tashi take yaganta tunda yayi wurgi da bra 'dinta.

Saidaya tattaro 'dan guntun kuzari ya mike ya fito ruwan ya fita
Saigashi da jallabiya fara tas ta maza da wani farin towel ya miqa mata ya juya dan idan ba haka yayiba taci gaba da zama gurin xai iyayin komai danko yanxu saidaya yaqi shai'dan sbd baita'ba jin sha'awa kamar yau 'dinba.

Goge jikinta tayi tana rawar jiki kafin ta xura rigar daya bata batareda ta tsaya 'daukar bra dinta ko sauran kayanba ta fito kanta na qasa ta fice da sauri harta tuntu6e.

Tunda take saukowa haj xeenay ta hangota amma ta kasa gasgata abunda idanunwanta suka hango mata.
Murza idanuwa tayi taga tabbas rigar tameer ce ajikinta kuma ga kanta a jiqe sharkaf da ruwa.

Wani rikitaccen gumi ta sharce tana jinjina kai har nazli ta shige 'daki.

Lallai nayi sanyi tunda har nayi saken da irin haka tafara faruwa.
Wlh babu tsinanniyar macen data isa ta haihu a zuriyar gidan nan tunda ban haihuba ko meenah bazan bari ta haihuba kozanyi yawo tsirara bare wannan shegiyar.
zanyi maganin komai
Kowama ya huta kona samu nutsuwar zuciya.

Adaren kasa bacci yayi sai juyi yake dan baitaba tunanin shi 'din mai cikakkiyar lafiya bane sai yau dan gabaki 'daya ya birkice buqace yake.

Ita kuwa zuru tayi akwance tana tunani me ciwo ko hawayen takasayi sai radadin zuciya.

⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜

Tunda wannan abun yafaru tafara 'boye masa.
Bata shiga aiki saiya fice hakama abincinsa tun bai dawoba take kaiwa ta aje ta ficewarta dan ta tabbatar da sonda take masa zai iya rinjayarta duk da ita tasan ba haramun bane to shifa?
Yazai 'dauki abun?

***********
Yau gidan ba kowa saisu sbd yaune suke bridal night amma fir tameer yaqi xuwa dan sam kamai na auren baya kansa.

Basusan dazai dawoba suka dawo gidan cikin isa da qasaita.
Nafisa haj xeenat takira a waya tace tafa'da mata tana neman nazli yanxu.

Fadawa nazli saqon haj xeenat tayi sukayi shiru cikeda tunanin me kuma zaifarune kaba komai yau batajin kanta daidai.

A daidai stairs suka tsaya nafisa tace,
Nazli duk abunda zasuyi miki kadaki yadda dasu dan zasuyita amfani dakene suna biyan buqatarsu.

Sawo kai yayi apalon cikin qasaita kuma kunnuwansa sun 'debo mai zancen nafisa na qarshe datace
" yadda dasu dan zasuyi amfani dakene gurin biyan buqatarsu"

Komawa nafisa tayi ita kuwa ta haye stairs 'din cikin faduwar gaba.

Tana shiga suka kalleta a wulaqance kafin haj xeenat tace,
Ba 'bata lokaci xamuyi ba abunda zamu da'da miki yanxu shine an canxa shara'di.

Ma'ana rayuwar fannah itace fansa ga rayuwar masoyinki.

😳😳 ja da baya tayi cikin muguwar ki'dima tana kallon bakin haj xeenat datayi xancen.
Haj kareema ta miqe tsaye tace,
Bari kada mu barki a duhu.fannah mukeson kisawa guba taci ta mutu idan kuwa ba hakaba to tabbas a daren farkonsa zaisha guba ya mutu.

Qwarai kuwa dan haka kiyi gaggawar xa'ba dan tafiya xamuyi.

Bushewa xuciyarta tayi tafara tunanin yanxu lokaci yayi daya kamata ta ringa tunani irin wanda su basayi sbd ku'butar da masoyanta daga sharrinsu dan tanajin qaunar fannah kaman yanda meer ke qaunarta amma zatayi wasa da tunaninsu dan tsirar dasu fannah.

Hawowa stairs 'din yayi dan xuciyarsa takasa nutsuwa aiko yana riqe handle 'din qofar xai shiga yayi dai dai data fara magana ya tsaya cak yana sauraronta.

ZAN BAWA FANNAH GUBA TASHA TA MUTU NIMA NA HUTA DAN NAGAJI DA WANNAN WAHALALLIYAR RAYUWAR.

Cikeda farin ciki suka miqe suka shige uwar 'daka batareda tunaninsu yabasu plan ne tayiba sbd sun san zatayi komai kan tameer.

Wani wawan jirine ya 'dibesa yayi saurin dafa bango idanunsa suka ka'da sukayi jajir
Wata mummunar tsanarta ta rufesa,
Qanwarsa dayafi so dakomai ita zata kashe masa da guba.

A fusace ya banka qofar ya shiga.
 Tsaye take riqeda qullin gubar dasuka bata sai wayarta dake hannunta tana shiein fitowa.
Duba palon yayi babu kowa sai ita ka'dai tana waya tana fa'dar kashe fannah xatayi.

Jikinsa har mazari yake ya shaqota xatayi magana ya 'daga hannu ya sharara mata kyakkyawan marin dayasa hancinta 6arewa da jini...

TO FAH.....

🌕🌕👉 mamuh geee
[7:39pm, 15/01/2017] Ⓜamuh geee: 🌕⚜DA'IMAN⚜🌕

Na
MAMUH GEEE

☆dedicated to☆
Husnah bbchoudiallo

176→180

Damqo hannunta yayi yafara janta zuciyarsa na tafarfasa.
Ji yake inama baije kunnuwansa suka jiyo masa itaba.

Jan qarfi yake mata ido jajir saidaya kaita tsakiyar palonsa ya wurgar da ita ta xube a qasa idanuwanta jajir sbd tashin hankali
Kukama sam baiga gurin xuwaba dan abun yafi qarfinsa.

Cikin karaji yace,
Ke wacece?
Me kikeyi anan cikinmu?
Meye dalilinki nason kashemun fannah?
Waya saki?
Wa kikewa aiki?
Wa.......

Jikinta rawa ya 'dauka tashin hnkalin da bata ta'ba jiba ya dirar mata ta matso ta xube a qasan kwance ta kama qafarsa a ru'de tafara fadin,
Wlh bazan ta6a cutatarda kai ba bare abunda nasan kana tsananin so,
Koba dan kai ba vazan iya cutar fannah ba sbd halaccinta gareni,
Dan allah kada kayi xargina walh bazan iya cutar......

Cakumota yayi jikinsa har rawa yake tsabar 6acin rai
Fuskarnan tayi jajir
Ya maqureta abango da qarfi yace,
Jst tell me d damn truth who the hell are u before i do sumtin crazy.

Duk tashin hankalin data shiga abaya baikai mata wannan ba dan yau tameer ne dakansa ke...
Jijjigata yayi da qarfi kamar qato dan uwansa
Sai alokacin wasu hawayen baqin ciki da takaici suka gangaro mata ba abunda takeso sama da

mutuwa alokacin.

Sakinta yayi ta xube qasa a zafafe ya bu'de fridge 'din palon ya 'dauko robar swan 'daya ya bu'de ya finciki qullin gubar ya fazge ledar ya juye acikin ruwan jikinsa sai cira yake
Ya 'dago hannunta yasa mata tana durqushe jagwaf sai hawaye take cikin baqin cikin kasancewarta araye hartaga wannan baqar rana.

Cikin wata irin tsawa da karaji yace,
Kince ba kasheta xakiyiba then prof yourself and drink it.

Qura masa ido tayi hawayenta na qara gudu ga idanun sun ka'da jajir sbd tashin hankali.
Cikin tsakiyar idanunsa take kallo gaba 'daya ya juye kamar wani xaki.

Prof me wrong and drink it idan kuwa ba haka walh i wont spare you
Hannun police xan miqaki harsai kin fadi abunda yasa kikeson kashe qanwata.

Tabbas rayuwarta batada wani sauran amfani gwara tasha ta mutu kowama ya huta itama ta huta da baqin ciki da wahalar rayuwa.

Kuka ta rushe dashi har tana shi'dewa hannu na rawa ta karbi robar batareda ta 'dagoba dan bata fatar sake ganin fuskarsa.

'Dagawa tayi ta 'dora abaki xatasha aka fixge robar da qarfi

Atare suka kai kallonsu gareta nafisace tsaye cikin tsantsar takaici tamaida kallonta ga nazli datake faman sheshshekar kuka ahankali kamar ranta zai fita
Cikin babbar murya tace,
Nazli lokaci yayi dazan daina kallon wannan masifar,
Me kike tunani xai faru idan kikasha wannan gubar kika mutu?

Me kike tunanin wa inda kikayi shekaru kina wahala sbd su zasuyi da rayuwarsu bayan sun gano ko ke wacece arayuwarsu?

Bakya tunanin ya rayuwar waleed xata kasance bayan kin mutu baki ha'dasa da mahaifinsaba.

Shin nazli meyasa bazaki daina wahala akan wa'inda basusan kinayiba?

Nazli lokaci yayi da sir ta......

Da sauri ta miqe da gudu ta nufi qofa tana wani irin jan numfashi sbd tsabar kukan datake.

Caraf ya riko hannunta batareda yakalletaba idanunsa nakan nafisa dake watso kalaman dasuka kusan tarwatsa masa tunani da qwaqwalwa.

Kukanta ke qara sauti kuma ahakan nafisa taci gaba da zancenta batareda ta tsayaba.

Nazli idan har kinasonsa kinason kare rayuwarsa to tabbas lokaci yayi dazaisan koke wacece.

Fixge hannunta tayi da gudu tana kuka sosai ta fice.

Jiri ya xubar dashi a kujera kansa na juyawa.
Qara hargitsewa tunaninsa yayi sbd bai gane komai na xancen nafisa ba amma ya gane abu 'daya shine zancensu nada alaqa dashi.

Duk yanda yaso tashi yabi bayansu jiri hanasa yayi sbd tashin hankali.

Da gudu ta isa 'dakin ta 'dibi kudin albashinta ka'dan ta fice gidan da gudu tana wani irin kuka mai tsima rai.

Tana fita tasamu taxi ta fa'da sai tasha kuma cikin sa'a mutun 'daya ake jira tana shiga suka tashi suka wuce har alokacin kuka take kamar ranta zai fita sbd ta rabu da tameer rabuwa tahar abada.

Tana shiga taga bata 'dakin ta duba toilet bata gantaba.
Fitowa tayi tafara dudduba ko ina amma babu nazli
Nan take hankalnta ya tashi tuni hawayen takaicin tameer da tausayin nazli ya tsinke mata sbd tana hango tsantsan masifa agaba muddin nazli tace ta tafi kenan kuma itama wallahi tafiyarta xatayi.

A ru'de ya sauko zashi 'dakinsu dan gaba 'daya yau idan basan komaiba komai xai iya faruwa dashi dan wata irin rashin nutsuwa yakeji kamar xaiyi hauka.

A firgice ta fito 'dakin tana hawaye suka ha'de bakin qofar ya wuceta xai shige cikin muryar kuka da takaici tace batanan ta gudu ta tafiyarta sbd kai,
Kaine sanadin komai na wahalarta arayuwa,
Meyasa ka kasa tsayawa ka fahimceta kayi mata wannan hukuncin harda baraxanar shayar da ita guba,
Shin ko kasan sbd kaine xatasha gubar tabar duniya duk dan sbd kai uban 'dan.....
Kasa qarasawa tayi sbd kukan dayaci qarfinta tace nima nasan koban tafiba xamana ya qare a gidannan dan haka tafiya xanyi.

Ido rufe ya daka mata wata mahaukaciyar tsawar dabaimasan yayiba ya bu'de ido jajir yace,
Har abada bazaki bar gidan nanba harsaikin fadamun abunda yake faruwa sbd xuciyata na gab da tarwatsewa sbd ru'du.

Cikin rashin tsoro tana sharce hawaye tace,
Ni 'yar aikice banida dama ko matsayin dazan fadi wani abu amma alh da haj da aminanta sunada dama harmada dr ibrhm.

Tana fadar haka ta shige 'dakinta ta sulale qasa tana kuka amma tasan allah bazai bari su cutatar da itaba tunda qarshen wahalar alamarin ne takawo idan har tameer yasan komai.

A zafafe yake kaida kawo apalon,
Banda sarawa ba abunda kansa keyi ga fuskarnan tayi ja abinka ga farin mutum.
Zama yayi a 'daya daga cikin kujerun palon yana jiran dawowar kowa daga gurin event 'din dan ayau yakeson jin komai basai gobe ba.

Sallamar dad ne da driver 'dinsa janye da 'yar jakarsa yasashi miqewa tsaye cikin godewa allah da dad 'din ya iso yau kuma a daidai lokacin dayake buqatarsa.

Kallon mamaki dad yake masa sbd ganinsa a yamutse hankali duk atashe idanunsa jajir.

Subhanallah tameer meyene naganka haka hnkli atashe?

Fitowarsu haj xeenat da aminan natane yayi daidai da fa'dar maganar dake bakinsa...

🌕🌕👉mamuh geee
[8:55pm, 15/01/2017] Ⓜamuh geee: 🌕⚜DA'IMAN⚜🌕

Na
MAMUH GEEE

☆dedicated to☆
Husnah bbchoudiallo

181→185

WACECE NAZLI A RAYUWAR NAN GIDAN?

alokaci 'daya jakunkunan hannuwansu su duka ukun suka kufce musu cikin wani irin mugun tashin hankali.

Kallonsu yayi yakaranto tashin hankalinsu tsaf a fili kafin ya maido kallonsa ga dad 'dinsa dashi kuma mamakine xalla afuskarsa na yanda akayi tameer yasan sunan nazli.

